□AUREN HADI□

✍M SHAKUR

EPISODE 1

DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

LUKU GENERAL ENTERPRISES LTD
Masu Kera Kayan Kamshi da Shayin Kamshi masu Inganci

Kara dandano da kamshi ga dafa-abincinku da jerin samfuranmu na Hamy:

Kayan Kamshi: Hamy Curry Mix, Hamy Ten Spice Mix, Hamy Garginion, Hamy Dawa-dawa Seasoning, Hamy Multipurpose Seasoning
Shayi: Hamy Black Tea, Hamy Green Tea, Hamy Spiced-Hibiscus Delight, Hamy Cassia-Tumeric Infusion

Dukkanin shayoyinmu an hada su da kamshi masu turare na musamman.

Adireshinmu: Unit 1 Block D, M.O.W. & Trans, Technology Incubation Centre, Bayan Gari, Bauchi, Jihar Bauchi

Don oda da tambayoyi, a tuntuɓe mu yau!

Instagram: #lukuku_ enterprise
Tiktok: Lukuku General Enterprises Ltd
WhatsApp: wa.me/+2348095660030

Babban falo ne hamshakin gaske da kamshin lafiyayyen turaren wuta ketashi, kana ganin falon kadai kai kawai kasan kudi sun zauna, ankumayi barin kudi awajen, mutane biyu ne rak a falon. Wani Babban magidanci wanda akalla zaiyi 65yrs ke zaune kan daya daga cikin kujerun falon, yanada jiki, yana sanye da manyan fararen Babban kaya, ga farin dogon gemu atare dashi, idanunsa sanye da glasses dakana gani kasan medicated ne, kai kana ganinsa kasan irin dattawan nan masu fadi aji, yanada wani irin kwarjini da haiba, fuskansa gabaki daya baya nuna farin ciki ga yar karaman pen a hannunsa yana rubutu akan wata yar takarda, gama rubutun yayi ya ijiye pen din a gefe saiya bude wata takardan check, yasake daukan pen din yafara rubutu aciki shima, tass yagama rubutun ya yage takardan check din ya ijiye gefe, ya dauki dayar takardan tareda check din yahada yarike yadago kansa yasauke idanunsa dake sanye da glass kan wata hamshakiyar mace dabazata wuce 40/41yrs ba in total, fara kal tana sanye da black abaya wanda mayafin ya zame ya koma baya kana ganin bakin gashinta dake kyalli yanada tsantsi, kana ganinta kaga balarabiya sak, idanunta sunyi ja alamun taci kuka duk tana kallonsa, irin kallon nan dake kauna da tashin hankali dakuma fushi, dan kada kafa yayi irin na manya tareda sauke ijiyan zuciya sannan cikin wata kalan muryan natsuwa da dattako daba hayaniya ko ihu ciki yace “ga takardan sakin ki nan Kutub” yadanyi shiru yana kallonta kaman yanda take kallonsa batako motsin kirki, yace “I write you check na 100M use it kifara wani abu” takai kusan 1min tana kallon takardun dayake mikamata saitakai hannuwanta tagoge fuskanta tass hacinta yayi ja sosai ta tako zuwa gabansa tasa hannu ta zare takardan sakin, cikin murya dake nuna fushi dakuma zuciya tace “karike kudinka banso Bello” ta fizge a zuciye, check din yabi da kallo saiya ijiye a hannun kujera yamike a nutse

yana gyara baban rigansa saiya wuce ta gefensa tabisa da kallo tana wani kalan nishi saikuma ta taho azuciye kaman zata dakesa saita tsaya dab dashi cikeda zuciya tace “you married me ina yar 20yrs, yau shekaranmu 21yrs da aure duk zaka zubar dashi? I don’t mean anything to you Bello? Baka tunanin Alhan?!” Chak yajuyo yakalleta cikeda izza yace “karki kuskura ki kira sunan diyata!” Tsayawa tayi tana kallonsa sai yanzu takara ganin tsananin bacin rai akan fuskansa, cikeda takaici yace “you should’ve thought of kinada diya kafin kiyi abubuwan dakikayi, sata Kutub? Sata!” Yadan lumshe idanu tareda sauke ijiyan zuciya yace “you have 2hrs to leave my house, the only reason i didn’t hand you over to the police is because of diyar dake tskanina dake, bazanso taga an kama mahaifiyarta ba duniya tamata dariya akan laifin mahaifiyarta ba, and also i promise i will pay back duka satan dakikayi, mutanen dakika cuta i will sort them out, just leave this house before I change my mind” yasa hannu zai bude kofan dasauri takai hannunta tadaura kan nasa hakan yasa yazare hannunsa takalli wajen zuciyanta na daci kyankyaminta yakeji komene, saita zagayo ta tsaya jikin kofan tana kallonsa cikin idanu kaman yanda yake kallonta tace “tayaya kakeso Ahlan tayi rayuwa agidan nan dakasan babu mai kaunar ta? She grew up a gidan nan da ba ruwan matanka da ita banda ta gaidasu su amsa, zan dauki y’ata natafi da ita” wani kallo yamata anutse yace “idan kinyi kuskuren tafiya da y’ata alokacin zan nuna miki waye Bello Makamo!” Wani kallonsa Hajiya Kutub keyi tama kasa magana sai hawaye dake fita daga idanunta, strictly Alhaji yace “tashi agabana”cikeda tsantsan tsana tadaki kirjinta tana kallon kwayar idanunsa tace “idan har naci sunana Kutub zanmaka alkawari daya wallahi sainasa kayi nadaman sakina dakayi!” Tadanyi shiru tana kallon kwayan idanunsa sosai kaman yanda yake kallonta tace “I will hurt you a inda nasan zaifi maka zafi, you call me criminal har kyankyanina kake ko? Zakaga criminal, wallahi zaka gani!” Tana maganan ta tashi daga gabansa tawuce ciki fuuuu yabita da kallo hartai sama sai kawai ya kada kai yabude kofa yafita, baban gidane da akwai flat gudu uku ciki, ga motoci, yawuce wajen wata Babban jeep inda driver dawani security su biyu ke tsaye aka bude masa bayan mota yashiga.
**

Bedroom dinta ta shiga tamaida kofa tarufe ta duka jikin kofan tana kuka sosai irin kukan nan mai ciwo, tadade ahaka saita mike tadauki wani LV akwati tabude saita bude wani drawer golds dinta ta kwashe gabaki daya tass tazubasu awajen ta kwashe su tamaida akwatin tarufe tadauki handbag din tafito saita tsaya dakin dake next to nata tabude kofan ahankali ta tsare dakin da idanu, ahankali ta saki hannun akwatin tasa tashiga dakin, very simple daki ne mai kyan gaske dayake a gyare amman akwai books akan gadon da laptop harda chocholate akan gadon, gawani dan karamin picture frame na gadon ahankali tawuce wajen tasa hannu tadauki frame din hoton wata yar yarinyar ce fara soll ta kankame Hajiya Kutub tana murmusi daya bayyana dimples dinta akan hoton, wasu sababbin hawaye ne suka shiga sauka akan hoton dasauri ta ijiye hoton tajuya tafita daga dakin takama akwatinta taja, tasauka kasa tabude kofan falo tafita, ko kallon sauran flats na gidan batayiba tawuce wajen wata faran mota Benz tabude baya tasaka akwatin sannan takoma gaba tabude ahankali tashiga tazauna tai jimmm tana fuzar da iska zuciyanta ba dadi kadan sai bin gidan take da kallo, sai chan ta kunna mota taja tazubama motan wuta bata tsaya ko’inaba sai Nile University, faculty of medicine tawuce direct, parking tayi batare data kashe motan ba dan AC na dukanta saita ciro wayanta daga jaka iphone 17, tabude dial calls dinta, number datai saving da BabyNoor tai dailing tasa a kunne har wayan yagama ringing ba’a daga ba, tana kokarin sake kiranta saiga kira ya shigo from BabyNoor daga wayan takai ta kara kunne kai tsaye tace “ina gaban department dinku ki sameni a mota” kawai ta katse wayan ta ijiye tana kallon gaban department din.
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 2

Hadadden auditorium ne wanda kowani dalibi dake ciki na sanye da labcoat, wani Malami namusu lecture. Wata black beauty yarinya ce dabazata wuce 20/21yrs ba itama sanye da labcoat takalli wata yar budurwa dake kokarin tashi tana ijiye pen na hannunta kan wani katon physiology textbook, atampa ne ajikinta red amman dayake tadaura labcoat akai bazaka gane wani style ne kayan ba, fuskanta sanye da nose mask, daga giranta wanda yake baki kirin kuma acike tum dogo yana kyalli sai idanunta farare tarr wanda suke dauke da dogayen bakaken gashin ido suma dogaye sosai kake gani kawai a fuska nata, sai skin nata dake nuna fara ce kal, yar bakan tace “ina zaki Ahlan”? Tai maganan tana whispering dan akwai lecturer a ajin kar ajinsu, dan dukowa tayi cikin wani kalan sanyin murya mai dadi wanda kanaji kasan ita ba mutum mai hayaniya bace tace “ina zuwa Husna, Ummy na kirana a waje” kafin kawar tai magana tajuya da dan sauri tashiga tafiya tana fita daga class din Allah yasa abaya suka zauna, Husna tabita da kallo yanda take tafiya tana rolling gyalenta daya warware tafita daga class dasauri ta tsaya tana gyara gyalen da kyau, yau ta manta batasa pin ta kama gyalen ba hakan yasa yake ja baya, one thing about her ko silin gashi guda daya bata tabaso yafito, she’s always properly covered.

Elevator ta shiga ta danna grand flour sai tunani take meya kawo Ummy school nasu yau, tana kaiwa kasa elevator yabude tafito tana tafiya, simple black cover shoe ne na zara a kafanta data saka black socks tafito tana tafiya a natse tana dumfaro parking space din, Hajiya Kutub ta tsareta da idanu, ba nose mask ba ko nikabi diyarta tasaka tasan yarta, Ahlan akwai natsuwa, she’s 20yrs amman tanada natsuwan manyan mutane shi kansa Abba yasha cewa kap yaransa Ahlan ce kadai tadauko natsuwansa, ita kanta tasan some dabi’u na Ahlan wlh ba ita takoyama yarinyar ba, tana sayama Ahlan kaya na yan gayu masu shape, but Ahlan bazata taba saka kaya dazasu kamata ba, ko su nuna jikinta ba, she wears safa, kayanta kullum are abayas, tasaka atampa to dole akwai labcoat akai tai rolling gyale bazata taba nuna gashinta ba, baruwanta dawani samari ko maza, bamata kallon mutane, batada surutu, ga hakuri, ita kanta tasan Allah yamata kyautan yarinyar nan ne a matsayin diya dan bata dauko halinta ba.

Anatse tazo wajen motan tasa hannu tabude side din mazaunin driver tana zare nose mask dinta Ya Rabbi!! Wata kalan faran yarinya ce, fara sol irin masu haske kaman yellow farin fatan larabawa ,kaganta sak mahaifiyarta, tanada wasu kalan mugayen pink lips kaman na jaririya masu bala’in kyau and moist, ga dogon hanci dan karami daya zauna a fuskanta portable, wani kalan smiling tayi daya lobar da dimple dinta sosai cikin wata yar karaman voice that’s so soothing tace “Ummy……” chak ta tsaya ganin idanun mahaifiyarta dasukai jaaa suka kumburo, dasauri takai hannunta zata taba fuskan Ummy, Hajiya Kutub tarike hannunta tanadan hade fuska tace “zagayo ki shigo ki zauna, maza” gyadama Ummy kai tayi ahankali tanajin wani iri abu a zuciyanta kawai kirjinta yahau dukan uku uku, tun tana yarinya ko mura batason taga Ummy tayi sabida jitke kaman zatai hauka, mood din mahaifiyarta na affecting dinta sosai, kawai she wants to see Mamanta koda yaushe smiling, zagayowa tayi tabude dayan bagaren motan ta shigo da sauri still tana kallon fuskan Mamanta idanunta har sun chanza launi ta zauna looking very very worried, kai tsaye tsaye tace “Ummy did you cry? Baki da lafiya ne”? Tai maganan tanakan hannunta wuyan Mamanta idanunta na ciccikowa da hawaye nan da nan, hannunta Hajiya Kutub ta rike takalleta strictly tace “bance kimin kuka anan ba, lafiyata kalau I’m not sick, waike bakisan kin girmaba eh, kuka baya miki wuya Noori”?

Daidai hawayen na karasa saukowa daga idanunta dasauri Ummy takai hannunta kan kumatunta ta sharce hawayen, asanyaye tace “Ahlan!” Wlh kawai jitayi bugawan da kirjinta keyi yakaru tarasa dalili, lips nata har rawa rawa suke tace “U….uhm….” Hajiya Kutub tai shiru tana kallonta, sakin da Alhaji yayimata yamata ciwo, amman tafiya dazatayi yanzu tabar Ahlan gidan nan da tasan babu mai kaunar yarinyar nan banda mahaifinta yafi komi mata ciwo, amman saita daure gently tace “Ahlan nazo nayi magana dake ne, ki saurareni” takai hannu takara share mata fuskan tass, rike kukan Ahlan tayi da kyar tana kallon Ummy batako kyafta idanu tanajiran maganan, Hajiya Kutub tadan sauke ijiyan zuciya tace “first of all inaso
kizama baban mace, ki iya kula da kanki, da kare kanki, da tsare kanki ko ina nan ko bananan, don’t let matan babanki bully you, ko yayyinki to bully you, ba koda yaushe ne I will be there to protect you ba Ahlan sabida for the first time arayuwanki, zakizo kifara rayuwan da babu ni cikinsa” wlh kawai gabanta sai faduwa yake Ummy na maganganun nan takasa daurewa, ahankali takama hannun Ummy tarike tana kaiwa chest nata tama kasa magana, dan lumshe idanu Ummi tayi, ahankali tace “mun rabu da babanki Ahlan, Babanki ya sakeni, I’m leaving his house!”
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 3
Dummmm! Kirjin Ahlan yawani buga kaman zai tarwatse jin abinda Ummy tace, tazaro idanunta masu kyau tana kara kakame hannun Mamanta a kirji tanama so tai magana yaki fitowa kawai kuka ya kufcema bakinta danshi yariga maganan zuwa, kuka take wanda all gabobin jikinta natayata yinsu, Ummy ta tsaya tana kallonta yanda take kuka kaman ita aka saka tama kasa cemata komi, da kyar ta iya lalubo magana a bakinta tace “yace nabar masa gidansa” Ahlan takara kara karfin kukan, dakewa Hajiya Kutub tayi tace “ke ba kuka nazo kimin ba, nazo nai sallama dake ne, dena kukan Noori” takai hannunta tana share mata fuska, kama hannun Mamanta tayi dake fuskan nata tana girgiza matakai, cikin wata murya da kuka yariga yaci karfinta tace “Ummy zan biki” dasauri Hajiya Kutub tace “so kike Babanki yasa akamani? Nima ai naso hakan amman bai yardaba, so a’a babu inda zani dake Ahlan, one thing I know is I will always be your mother, babu abinda zai rabamu kinji, ya isa dena kuka” ina ko alamun tsayar da kukan batada shirin yi, Ummy tai shiru tana kallonta sai kawai ta matso tajawota jikinta ahankali tace “come here My Noor” kankameta Ahlan tayi dasauri tana kara rushewa da kuka sosai a kirjinta tace “Ummy ni karki tafi ki banni, ni zan biki, muje muba Abba hakuri zai hakura yabari nabiki” dan murmushi Hajiya Kutub tayi tana shafa bayanta tace “karatun ki kuma fa? Bakisan harda ganin kina medicine yasa matan Babanki kara tsanan kiba, banda haka saki ba abin wasa bane Ahlan, aurena da Babanki yakare babu any magic dat can amend that, kawai yanzu kidena kuka I will be fine, me and you are just about to start another different life wanda bana cikin naki, kema baki cikin nawa, I know at first bazakiji dadin rayuwan ba but I will come and get you nan gaba kinji, i promise” cikin kuka tafito daga jikin Ummy ahankali cikin rinannun idanunta tace “meya hadaki da Abba Ummy?” Dan jimmm Hajiya Kutub tayi sai chan tace “I’m not ready to talk about it, let’s just say bayason side hustle dina, he wants me to depend on him, he should be komi da komi nawa” baki Ahlan tabude zatai magana Hajiya Kutub tace “don’t ask me anything again, Menene kalman danake yawan gayamiki?” Ahankali Ahlan tace “kome Ummi tace shine gaskiya” gyadamatakai Hajiya Kutub tayi saitai murmushi takama bakin gyalenta saita jawo fuskanta tashiga sharemata hawayen tace “yanzu abinda nakeso is ki share hawayen nan go back to class, I will always be your mother, nobody can take me away from ur life, wuce kitafi class” wani sabon kuka tarushe dashi batai motsi ba, Hajiya Kutub tahade fuska strictly tace

“wuce kifita ki wuce aji, banson shirme Ahlan” tana shakkan mamanta especially idan babu fuskan wasa, ahankali ta yunkura tana kuka tana kallon Ummy kaman wacce ke jiran Ummy tace mata wani abu amman harta tabude kofan Ummy bata cemata komiba, dan waigowa Ahlan tayi tana kallon Mamanta, kana ganin yanayinta irin yaran nanne dakeda tsoron iyayensu kuma suke mugun son iyayensu, fita tayi ta tsaya tana kallon motan batare data rufe kofan ba, Hajiya Kutub tayi tsareta da idanu bata cemata komiba kusan 1min suna ahaka saita yunkuro takai hannu tarufe takama kofan tai jimm tana kallon yanda Ahlan ta tsaya tana kuka sosai gabaki daya tama manta a school take, batadamu da kowa ba kuka take harda haki, wani irin ajiyan zuciyan Hajiya Kutub tayi kawai ta fuzar da iska tadauke kai batare data kalli Ahlan ba tarufo kofan motan takoma ta zauna da kyau ta kunna motan taja tabar wajen Ahlan na kuka sosai tadaura hannunta abaki tanabin motan da kallo har saida tadena ganin motan sai kawai taduka awajen ta kifa kanta akafa komi na duniya yadena mata dadi.

Tama kasa imagining rayuwa babu Ummy ba, is she dreaming? She left gida this morning Ummy da Abba were literally gisting while having breakfast a falo, toh meya hadasu? Meya faru da Abba? Bata taba ganin Abba da Ummy na fada ba tunda aka haifeta bata taba ganinsu suna fada akan idanunta ba wlh saisa taji zancen wani iri, kaman ba gaske ba kaman she’s day dreaming, kawai jitayi duniya nan ya dayamata chak, batada any damuwa arayuwanta, she’s always happy, tana karatu sosai, she’s in her 4th year medicine, suna aiki a hospital, she still goes to islamiyya on weekends, Ummy is the one coordinating rayuwanta for her, tayaya zatai rayuwa ba Ummy aciki? She even imagine it at all, dafata akayi “Ahlan, Ahlan” dago kanta tayi da jajayen idanunta, ganin idanunta akidime Husna tace “Innalillahi menene ke kadai kike kuka anan eh? What happened Ahlan”? Bayan hannunta takai kan fuskanta ta share saita mike tsaye, Husna tace “what happened Ahlan kinma Ummy laifi ne? Ga jakanki mun gama lectures din?” Hannu takai ahankali ta karbi jakan another new set of tears na rolling suna saukowa kawai tawuce dasauri tashiga tafiya Husna nabinta dasauri itama suka wuce masallaci, tana shiga mosque din bangaren mata tawuce chan karshe kawai ta kwanta takifa kanta, Husna tashigo masallacin daba kowa ciki dan is 3 o’clock yanzu na rana, tsayawa tayi akanta tana kallonta idan dasabo tasaba, Ahlan bazatai magana ba cus wata kalan shiru shiru ce, kawai batada hayaniya, tundaga year one suka zama friends but a year four dinnan ne Ahlan kemata yar doguwan hira, sometimes she don’t really blame her sabida yarinya ce wacce batada any siblings dasuke ciki daya, she’s always on her own kotana gidansu, inba Ummy taba babu mai hira da ita agidan, taga step sisters dinta, tsakaninsu saidai Ahlan ta gaidasu su amsa da kyar shikenan maganan tsakaninsu, sometimes Ahlan na bata tausayi.

Ajiye jakanta tayi tazauna ahankali kusa da ita, dudda sunada another class very important class but she can’t abandon kawarta like this, hannunta takai ta daura a kafadanta tace “you think abinda kikemin is right Ahlan? I’m your friend something happened to you, kinki fadamin tun a parking space kike kuka, did something happen to Ummy dakika ce takiraki? You’re not talking to me I’m worried, Ahlan!” Husna tadan kirata da karfi sanin bakoma a masallaci har a side na maza war haka bakowa a mosque, bakajin karan kukan datakeyi amman jikinta na kakkarwa na sheshekan kuka, kai dayan hannunta Husna tayi tadaura akan kafadanta saita dagota tace “sit up” batai musuba tasowa tayi ahankali takalli Husna idanunta sunyi jajir, Husna takai hannunta dasauri tana goge mata fuska hankalinta yatashi sosai tace “Ahlan menene is Ummy sick?” Girgizamata kai Ahlan tayi, Husna tace “to menene”? Kaman jira take wannan karan saita fashe da kuka sosai mai dan kara tana kallon Husna, Husna tace “what happened at home Ahlan?” Cikin kuka da yar muryanta daba kwari tace “Abba ya saki Ummy na”….

Chak ya tsaya jin wata murya mai rahaman dadi daya sauka akan kunnenshi ya daki tsakiyan kirjinsa daidai yana kokarin fita daga mosque din, just like that hakanan yaji abu kaman yarikemai kafa ya tsaya gaban kofan batare dayasa kafa ya idasa fita daga mosque dinba……..

Ahankali Husna tace “Innalillahi wa innailaihi raji’un, Abba dakeji da Ummy, are you sure kuwa?” Gyadamata kai Ahlan tayi still crying tace “yace tabar gidan, she came to tell me she’s leaving, Husna Ummy is the only one I have agidan……”
Ahankali batare dayayi making any sound ba yasa kafa yafita cus he feels kaman he’s invading privacy yaran nan dayaji suna magana that seems very personal kan iyaye, wani exquisite takalmin Armani yasa kafafunsa ciki da kumbunansa farare gyararru suka kara haska takalmin, yafara tafiya hakanan kaman abu na fizgansa saiyaji he wants to see wacce ke cikin damuwan mai kukan da aka saki Mahaifiyarta, tafiya yashigayi saiyadan juya yakalli glass na window side din matan wanda zaka iya ganin kowaye aciki dan is transparent glass, mata biyu yagani dukansu sanye da labcoat, Husna na rungume da Ahlan da fuskanta ke kirjin Husna tana kuka jikinta na rawa na sheshekan kuka, all he could see was hannayenta dake bayan Husna sabida hugging nata datayi, fararen hannu ne masu dogayen yatsu da dogayen kumba da akwai jan lalle a half na kumbunan ta, sai wani dan warwaro na golden beads guda daya rak a left writs nata. “Uncle Habeeb!” Sukaji muryan namiji dayasa ba Husna kadaiba ita kanta Ahlan saida tafito daga jikin Husna daga ita har Husna suka juya suka kalli Window wani namiji suka gani yabama window masallacin baya so basa ganin fuskansa amman fatarsa bakace, mutumin is very huge and tall, yana sanye dawata ash short sleeve riga dake nuna huge murdadden muscles nasa exactly irin na yan wrestling, wani yaro wanda bazai wuce 16yrs ba dan tuliki yazo da gudu yawani rungume sa yace “Uncle Habeeb i thought you were pranking me dakace nazo school mosque namu zan ganka” cirosa yayi daga jikinsa batare daya juyoba cus yasan by now dole yaranchan sunji muryan Areef sun juyo, cikin murya kasa kasa yace “let’s go Areef”.
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 4
Areef baiyi musu ba yabisa suka bar wajen yace “when did you arrive Nigeria Uncle Habeeb”? Ahankali yace “just now, from airport nazo nan” wani tsalle Areef yayi yace “i love you Uncle Habeeb dina” dan murmushi kadan yayi baiyi magana ba, Areef yace “da Bolt kazo school namu”? Anatse yace “nope” cikeda surutu Areef yace “how did you get car kazo nan”? Kaman bazaiyi magana ba suna tafiya chan yace yace “Ibrahim came to pick me up” zaro idanu Areef yayi dasauri yace “Uncle Ibrahim” parking space sukaje wajen wata arniyan Lexus, Habeeb yabude baya yakalli yaron cikeda so yace “get in” shiga Areef yayi yazauna yana kallon mutumin dake mazaunin driver wanda kusan kansu daya da Habeeb kawai Habeeb zai nunamasa tsayi da murdadden jiki ne, sai kuma shi yanada haske unlike Habeeb da bakine yace “Uncle Ibrahim good afternoon” kallon Areef yayi yace “Kiddo ya akayi? Ya school din”? Zagayowa Habeeb yayi yabude kofa yashiga yazauna yana danna wayansa, Ibrahim ya kallesa yace “ina mukayi”? Batare daya dago kansa ba yace “where do you want to go Areef”? Dadi kaman zai kashe Areef yace “Uncle there’s this new gaming place da aka bude i told Daddy yakaini but yace baida time nan nakeso naje” Ibrahim ya kallesa yace “bakasan yanzu yadawo ba he needs to rest” sanyi jikin Areef yayi asanyaye yace “muje gida to” daidai lokacin yagama danna wayan yadago kansa ya kalli Ibrahim yace “lets go to duk inda yakeso muje” Areef

yayi wani ihu, Ibrahim ya hararesa ya kunna motan, Habeeb bai kara magana ba sai kallon waje yake, har sukakai wajen yabiya Areef yayi duk abinda yakeso yasami waje yazauna yana kallon Areef duk Ibrahim na kallonsa, saiya taho inda yake zaune yazauna gefensa, ahankali yace “Hey” dan kallonsa Habeeb yayi baiyi magana ba yakai hannayensa yana tattaba aljihu saiya kalli Ibrahim daya dauke kai abinsa, Habeeb yayi shiru chan kuma da wannan manly dark voice dinsa yace “you will buy that cigarette daka dauke”calmly Ibrahim yace “you left Nigeria back then Areef was just 8yrs old look at him today he’s 16 a whole adult, you still smoke Habeeb”? Wani kallo Habeeb yamasa idanunsa na kadawa suna chanza launi sai kawai yamike yace “I’m going outside to smoke” kama hannunsa Ibrahim yayi a sanyaye yace “Alameen!” Tsayawa chak Habeeb yayi sabida girman sunan nan duk sanda aka furta sunan kome yake saiya natsu sabida darajan wacce ke kiransa da sunan a zuciyansa, Ibrahim yace “I know you’re hurt, I know Baba yayi kuskure daya koreka daga gida but look at your life now, look at you today, you’ve turned your life around and become a better person wanda 8yrs ago bahaka kake ba you…” Ibrahim yadan sasauta muryansa yace “nasan babu excuse akan mahaifin daya kori dansa daga gida, but kana tunanin da ba’ai hakan ba would you have been able to change? To grow yourself? Have you seen how far your tech company have come? You have a branch a US anan Nigeria, kasan Baba is one of your biggest fan”? Wani kallo Habeeb yamasa sai kawai ya tashi zai wuce batare dayace wani abu ba dan baida even a single interest akan maganan, hannunsa Ibrahim yarike wani kallo Habeeb yamasa kaman zaki dan yanada mugun zuciya hakan yasa Ibrahim yace “wat? You want to fight? Habeeb please common buddy, for the sake of Ammi” azuciya yace “don’t you dare bring Ammi into this!” Ahankali Ibrahim yace “please Habeeb please, i know Baba yayi kuskure da dama, he has been calling you baka daukan wayansa, yayinka baka magana dasu, ka yanke alaka da kowa, it’s time to return home and settle down, family is everything”dan lumshe idanu yayi trying to calm down strictly yace “I’m only here because Ammi is sick Ibrahim, I wanted to see Nephew dina first, and head back to UK tomorrow saisa the only abinda nazo dashi is my passport” yataba aljihunsa da passport din yake, yace “kadena min maganan that politician man” yajuya azuciye yace “idan Areef yagama I’m outside” yafice daga wajen yana tafiya kaman wani zaki yafita har zuwa wajen motan ya dafa motan tareda runtse idanunsa dasukai jajir yana fuzar da iska yakai kusan 2min ahaka saiya dago kansa yashiga tafiya zuwa wani shago dake wajajen idanunsa still sunyi ja da hannu kawai yanunama mai shagon kwalin taba baida naira yadauki 100dollar note yabasa kawai yajuya mutumin yace “nagode yallabai” ko juyowa baiyiba, komawa wajen motan yayi yabude kwalin taban yazaro kara daya yakai baki yatura kwalin taban aljihu, yarike taban a hannunsa yadan lumshe idanu batare daya kunna ba, to be honest he can’t remember the last time dayasha taba ko shisha ko wani abu, tunda Mahaifiyarsa tarasu Umma shikenan yakasa cigaba wa, but you will always see him da kwalin taba, especially idan ransa yabaci zai saka abakinsa kawai yayi shiru hakan calm him down, now that’s the last phase na addiction dinshi dayake fighting yadena samin comfort da natsuwa a karan taba, yadena sha but he’s always with it kaman active smoker.

Hango Ibrahim da Areef yayi suna fitowa hakan yasa yazare taban daga bakinsa ya jefar, suka karaso wajen da gudu Areef yazo wajensa yace “are you okay Uncle Habeeb? Your eyes sunyi ja?” Kansa ya shafa yace “really maybe wani abu ya shiga ne, let’s go” yabude masa baya Areef yashiga yamaida kofan yarufe yakoma gaba yazauna baicema Ibrahim komiba, Ibrahim ya kunna motan yaja a hanya suka farayin magrib sannan suka dawo suka shiga motan suka wuce.
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 5

Wani arnen mahaukacin estate sukayi, estate guda ne kuma na mutum daya duk gidan mahaifinsa ne, yan sanda everywhere, all his brothers duk wanda yayi aure ciki suke zama, rabonsa da gidan nan 8yrs kenan, so many changes, anyi renovating so many things, memories sai dawomai yake from when he was small, gate kusan guda uku aka bude sannan sukakai asalin compounds din wanda manya manyan flat flat ne sunfi a kirga ciki masu style da yanayin gini iri daya, Ibrahim yayi parking yakalli Areef yace “tafi” saiya kalli Habeeb daya lumshe idanu, asanyaye yace “let’s go Ammi is waiting” dan bude idanunsa yayi ahankali saiya juyo da kansa ya kalli wani flat wanda yake na tsakiya yay shiruu saiya dauke kansa yakalli agogon hannunsa yace “muje I will see Ammi in 10min and leave” Ibrahim baice masa komiba yabude motan yafito saida yazagayo ya tsaya jikin motan sanna Habeeb yabude yafito ahankali wani sanyi yaji a tsakiyan zuciyansa, maida kofan motan yayi yarufe ahankali sannan yashiga tafiya yana biye da Ibrahim.

Ko kallon Babban flat na gidan baiyiba yamazo yafi Ibrahim sauri yawuce flat na uku saiya tsaya jim batare daya bude kofan ba, Ibrahim ne yabude kofan ahankali da sallama kamshin turaren wuta yafara musu oyoyo, wata babban mace mai dan jiki ne tsaye cikin falon tana sanye da kaya na mutunci masu kyau da kayatarwa ga kanula a hannunta na drip tace “ina Alameen Ibrahim”? Matsawa gefe Ibrahim yayi hakan yasa idanunta suka sauka akan Alameen dake tsaye gaban dakin bai shigoba kansa akasa ta tsaya turus tana kallonsa idanunta na cicciko da hawaye sosai rabon data sakasa a idanu shekaru takwas kenan, tama kasa magana sai hawaye, ahankali bakinta na rawa tace “Alameen” ahankali yadago kansa yadaura su kan Ammi wacce duk duniya she’s the second person he considered a mother bayan mahaifiyarsa cus tamai abinda duk wata uwa zatama danta aduniya, today is the first time yake ganin alamun tsufa sun bayyana tattare da ita, wani iri zuciyansa yayi especially yanda take kuka tana kallonsa tama kasa magana ga canula a hannunta, shigowa dakin yayi yataho har gabanta ya tsaya zaiyi magana kawai Ammi hugged him cikeda tsantsan so da kewa da lot of emotions, wani sanyi jikinsa yayi kaman kankara yakasa ko motsin kirki, ahankali yadaga hannuwansa duka biyun yadaura abayanta cikin wata murya mai sanyi kaman batasa ba yace “kiyakuri Ammi!” Kanajin yanda yayi magana kasan he has a very soft spot for her azuciyansa, ahankali yace “I’m sorry Ammi” fitowa tayi daga jikinsa ahankali takallesa idanunta sunyi jaaa suna tsayaya tace “kalaman karshe da Yaya (haka ake kiran mahaifiyar Habeeb) tabani kafin ta dauki numfashinta na karshe shine tabani amananka, na tsaya maka, na taka rawan uwa a rayuwanka, amma ba yanda banyiba shekaru takwas currr saiyau nake daura idanu akanka sabida banda lafiya Alameen eh? Sabida banda lafiya daba hakaba da harna rasu bazan ganka ba? Ka kyauta?” Ammi tai maganan tana dan makan hannunsa ahankali cikeda so tana kuka still, sauke kansa kasa yayi, bude kofan dakin akayi wata wacce ke kama da Habeeb ce tashigo tanada dan jiki itama Babba ce dawani kalan sauri tazo wajen hannunta tadaura saman hannunsa ahankali tace “Habeeb” juyoda kansa yayi yakalleta yazuba mata idanu batare dayace mata anything ba saiya dauke kansa yakalli Ammi gently yace “muje ki zauna Ammi” anatse Ammi tace “bazakama yayarka Zainab magana ba”?

Dan lumshe idanu yayi yabudesu ahankali yace “ina yini Ya……” hugging nasa Ya Zainab tayi ta side sosai kafin yama karasa maganan sai kuka tama kasa magana Ammi ma tacigaba da kukan turo kofan aka sake yi dasaurin gaske da sallama, Alhaji ne sanye da manyan kaya yana rikeda hannun Areef saikuma Babban dansa wanda yake kama da Habeeb sosai amman Babba ne yanzu yana neman 48yrs duk suka shigo, bugawa kirjin Alhaji yayi daura idanunsa dayayi kan dansa Alameen, ya tsare Habeeb da idanu wanda yaki kallon inda suke ma, yadaga Ammi daga jikinsa

yakamata yakaita kujera saiya zaunar da ita saiya duka gabanta cikeda caring, hannunsa yakai kan fuskanta ya share fuskan tass yamata wani cute smile Alhaji na kallonsa bayako kyafta idanu kaman yaune rana na farko daya fara ganinsa a duniya, ahankali yace “stop crying Ammi, bari natafi, take care of yourself Ammi, Allah kara miki lafiya”yadago kansa ahankali yadan kalli yayarsa Zainab dake kallonsa tana share hawaye saiya dauke kai ya mike tsaye a nutse yajuyo ko kallon Alhaji dake kallonsa bayako kyafta idanu baiyiba yataho yana tafiya kaman zaki yazo ta gefe zai wuce bai kalli babansa da wansa ba, cikin wata kakkausan murya Alhaji yace “bakaga mahaifinka anan bane ko kanada wani mahaifin daya wuce ni?”Baice komiba yacigaba da tafiya zai fita kawai Alhaji yasha gabansa hakan yasa Habeeb ya tsaya chak, babu wanda yace wani abu a dakin cus deep down kowa in that room nason wanna matsalan yakawo karshe so suyi bala’in dazasuyi yau takare, cikin fushi Alhaji yace “you know duk cikin yarana ku goma sha biyar kai kadaine kadauko halina Habeeb, taurin kai, bakin zuciya, fushi da ruko dan haka daidai nake dakai, and I will tell you one thing listen very carefully kaman yanda nine na koreka from this house this time nine zan hanaka fita daga this house, you are not going back to US assign whoever you want to assign acigaba da kula maka da company ka till further notice, I’m running for presidency I need all my families with me banda haka it’s already settled aure zanmaka!” Tunda Abba ke maganganun nan this is the first time da Habeeb yadago fuskansa yakalli mahaifinsa ido cikin ido, shima haka Abba kallonsa yake babu wani tsoro ko shakka, and shima he’s a very strict father kawai Habeeb ne ya kangare masa duk cikin yaransa saisa ya koresa yanzu kuma yayi alkawari he will bend him, infact Ammi lafiyanta kalau dan Maleria ce tayi shine yacema Dr ace Ammi has cancer hakan zaisa Habeeb yadawo.
Cikin wani Husky harsh voice Habeeb yace “kulleni zakayi agidanka kome?” Sosai Alhaji ke kallonsa Habeeb murdadden stubborn fearless yaro ne, kap yaransa Habeeb daban ne, shima Alhaji cikin taurin zuciya yace “kulleka in this 2026?” Yanuna muscles din Habeeb yace “with all this big muscles daka tara ai ko securities dina guda goma banjin zasu iya kaika kasa ba balle ma ayi zancen kulle ka, so Alameen no ba kulleka zanyi ba, but I want to show you ni dinnan nina haifeka, my blood runs through veins naka, kadawo gidan nan kadawo kenan forever, idan kadaga kafa kabar gidan nan ni mahaifinka Ya Allah kana gani ban yafe masaba har lahira” dasauri Ammi tace “Alhaji!”Dagamata hannu Alhaji yayi azuciye hakan yasa tai shiru deep down itama batason Habeeb yakara tafiya and she knows sometimes wuta saida wuta, cikin tsananin fada Alhaji yace “you think because you’ve grown muscles I will be afraid of you? Bari kaji ni kalan iyayen nanne da I can never ever be afraid of danda na haifa kowaye shi, I will trash you Alameen, give me your passport”? Alhaji yafada da karfi, kallon Babansa Habeeb yayi da idanunsa dasukai jajur hannuwansa har rawa suke cikin wani kalan murya mai balain zafi ba tsoro yace “you stopped being my father from rannan daka koreni nabar gidan nan I am not giving you passport dina” Alhaji yadaki kirjinsa yace “wallahi Billahillazi azeem saika bani passport dinka Alameen bazaka kara barin Nigeria ba” wani tsawa Habeeb yayi yace “bazan ba…..” “Innalillahi wa innailaihi raji’un…” Ammi ta yanke jiki tafadi bawai da gaske ba but she’s just doing it sabida Habeeb, atare Habeeb da Abba suka kalleta dawani irin sauri Habeeb yatarota duka yaran kowa yayo kanta, kowa yace “Ammi, Ammi” Alhaji yace “wife wife” wani kalan fashewa tayi da kuka tace “zaku kasheni zan mutu Habeeb zan mutu” Dasauri ya girgizamata kai the way tayi is triggering so many memories on him tace “Alameen mahaifinka kakema ihu kasan cewa fushin Allah nadaga cikin iyaye hakama yardansa, mahaifinka kake gayama ba mahaifinka bane kanada wanda yafisa? Mahaifinka ko boka ne hakki ne akanka kamasa biyayya inhar ba wajen sabama mahallici yace kayi ba” cikin sassanyar murya yace “stop talking Ammi” ahankali tace “toh Alameen amman inaso kanunamin na isa nakuma kai mahaifiya agareka, idan har na isa dakai Alameen kabasa passport dinka!” Dasauri yace “Am….” Girgizamai kai tayi hawaye na gangarowa daga idanunta tace “cewa nayi idan har nakai nakuma isa mahaifiya gareka kabasa” yakai kusan 1min

yana kallon Ammi dake hannunsa extremely weak bai bada passport dinba, Ammi tace “mahaifiyarka bata raye, baka lafiya da mahaifinka, nima zaka nunamin ban isa dakai ba? Habeeb bakaso ka kare da duniya lafiya?” Dan huci yayi da ita kanta Ammi saida taji yanda numfashinsa yayi zafi sai kawai yakai hannunsa yataba aljihunsa yaciro international passport dinsa yajuya yakalli Alhaji dake kallonsa shima fuskansa ba alamun Rahama yamika masa passport din, hannu Alhaji yasa ya fizge passport din kawai yajuya yace “lemme go call your Dr wife” yawuce yafita babu wanda baiji dadin karban passport dinsa da akayiba atleast ansan baya kara barin kasan, har Alhaji yafita daga dakin saiya bude kofan yadawo yakalli Habeeb babu wasa kan fuskansa yace “lastly ka shirya aure zan maka cikin watan nan! You will be getting married to diyar aminina wanda zai fito amatsayin Vice President dina atara, she’s in med school” Alhaji na maganan yajuya yafita yabugo kofan bammm!
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 6
Ganin mutanen sun wuce yasa Husna tace “ashe akwai mutane, muyi magana kasa kasa” hannuwanta guda biyu takai kan fuskan Ahlan tace “Ahlan komi na duniya dakikaga yafaru Allah yariga yarubuta hakan zai faru tun a lauhul mahfuz, now what I want you to do is kidage da addu’a Allah ya daidaita tsakanin Abba da Ummy, sannan now that ba Ummy ki agidan stay out of trouble, baruwan ki, anything they will say to you don’t answer them, leave peacefully just focus on school give it time zakiga zasu dawo su shirya kinji” gyadamata kai tayi ahankali, Husna tace “bakomi Allah na tareda ke, okay” dudda tana cikin mugun damuwa but maganganun Husna comforted her saita kara gyadamata kai, murya chan tace “thank you Husna” murmushi Husna tamata tana patting back dinta ahaka har akai la’asar driver su yazo suka fito suka wuce parking space, gaban wata arniyan latest sienna sukaje, driver na tsaye wani dan Dattijo yace “idanunki na ciwo na Ahlan”? Ahankali ta girgizamai kai tace “ina yini” saita shiga motan inda wasu yan mata guda biyu ke ciki matasa da zasu dan girmeta, suna zaune suna taba waya, ahankali tawuce su zuwa chair na bayansu tasami waje ta zauna daya daga cikinsu ta tabe baki, dayan kuma ko dagokai batayiba, driver yarufe kofan motan yazagayo ya shiga gaba yaja motan. Harsukakai gidansu babu wanda yay magana a motan, bude gate akayi suka shiga akai dogon tafiya kafin akai second gate, aka bude driver ya shiga, tunda suka shiga gidan idanunta nakan flat dinsu, babu kowa a compound din banda ma’aikata, parking driver yayi yanmata biyun suka fara saukowa suka wuce abinsu, sai ita tasauko ahankali tafara tafiya ahankali tawuce flat dinsu, zuciyanta na gayamata maybe is all a dream tana bude kofa zataga Ummy a falo, tabude kofan babu kowa falon dan jim tayi saita shiga ciki tamaida kofan ahankali tarufe tashiga tafiya ahankali tana kallon falonsu abu ya tsaya mata a wuya gani take kaman komi mafarki ne baki tabude kaman mai shakku murya chan kasa tace “Ummy” shiru ba wanda ya amsa, kitchen dinsu tawuce tabude taga bakowa ciki saita maida kofan tarufe sannan tawuce sama tana tafiya ahankali hartakai sama, direct dakin Ummy tabude taga dakin bakowa sai kawai taji idanunta sun ciko da ruwa sun mata nauyi sosai kawai saita fashe da kuka cus wani iri abin kemata, it feels unreal bata taba imagining wai Mamanta zatabar gidan nan ba ko Abba zai rabu da Ummy ba, to wa takeda shi yanzu a gidan nan bakowa? Dukawa tayi ahankali ta sulale tazauna awajen saita bude jakanta taciro wayanta number Ummy tai dialing amman gabaki daya wayan bayama shiga at all, takara dialing number hawaye har diddiga yake yana sauka akan wayan still baya shiga, Mamanta is her everything, tana zaune awajen har aka fara kiran sallan magrib, ga yunwa tanaji da kyar ta mike tsaye fuskanta ya kumbura tabude kofan dakinta ahankali ta shiga, jakan school nata ta ijiye tazare labcoat na

jikinta ta ijiye sai tawuce bayi ta dauro alwala tafito ta shimfida dadduma tasaka hijab tai salla tana idarwa tasake daukan wayanta tai dialing number Ummy still baya shiga kirjinta kawai bugawa yake ijiye wayan tayi a gefenta tai hugging kafafunta tana kuka wanda hawaye kawai kebin kuncinta.

Around 7:30 motansu yayi parking cikin gidan dasauri bodyguard yabude mai motan, fitowa Abba yayi a tsanake sai yayi jimm ya tsaya yana kallon flat dinsu Ahlan, kafin yakalli security yace “take the files inside” dasauri yace “yes sir”anatse yake tafiya yanadan dingishi dan kafarsa daya ba lafiya yawuce flat din da kansa yasa hannu yabude kofan falo da sallama a natse yana bin ko’ina da kallo idanunsa suka sauka kan check daya rubuta dazu, karasawa yayi ya tsaya a wajen saiyakai hannu ya dauka ya linke yasa a aljihu saiya wuce sama yana tafiya cikeda kasaita harya karasa saman, kai tsaye gaban dakin Ahlan yayi a natse yadaga hannunsa yayi knocking sau daya tareda magana. “Assalamu Alaykum” shiru ba’a amsa ba, hannu yasa ya murza kofan ahankali yabude kofan idanunsa suka sauka kan Ahlan dake kan dadduma bacci yayi awon gaba da ita ga hijabin data kwabe a gefe, ga jakan makarantan ta a gefe da labcoat ga books nata akan kujera, kanta ba dan kwali kalaba ne akanta duk sun warwatse ga tsayi sosai gashinta baki kirin yana kyalli, tsare fuskanta yayi da idanu, tip na nose nata yayi ja, hers eyes sun kumbura alamun tasha kuka yayi jimmm yana tunani, anatse yace “Ahlan” firgigit tabude idanu saita tashi zaune da sauri ganin Abba takai hannunta tadaura saman kanta jin ba kallabi saita daura hannunta ka gadon tadauki gyalen data cire tayafa aka, jikinta nadan rawa kadan, kanta akasa ahankali tace “Abba sannu da zuwa, ina yini” kana ganin yanda takeyi kasan Abba mutum ne da yaransa ke shakkan sa sosai, a nutse Abba yace “kinci abinci?” Girgizamai kai tayi alamun a’a tace “a’a” har lokacin kanta akasa tana wasa da yatsunta, dan jimmm Abba yayi yana nazarinta ba alamun wasa kan muryansa yace “tashi ki hada yan abubuwan amfaninki zaki koma wajen Mamanki Hajiya da zama, ina jiranki a falo” gyadamai kai tayi asanyaye tace “toh” yajuya ahankali tareda sa hannu yajawo mata kofan yawuce a nutse yashiga sauka daga staircase din yawuce falo yazauna yana jiranta.
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 7
Wani irin kuka mai daci da kunci yataso mata, duk yanda zata musulta abinda takeji a kirjinta yanzu haka bazata iyaba, tunda aka haifeta bata taba kwana awani waje daya wuce dakin mahaifiyarta ba wato nan flat nasu, Ummy bata barinta shige shige, iya kata da dakunan su is zuwa gaidasu everyday dasafe shima sabida sharaddin da Abba ya kafane son Mamanta ne shima din da bazata barta taje kawai ba yanda zatayi da Abba ne, duk yaron gidan saiyaje ya gaida step mom dinshi in the morning everyday banda haka Ummy bata barinta zuwa ko’ina, daga boko sai Islamiyya sai gida, idan tana gida kuma she’s reading, Ummy control her life and program all her activities, ko friends bata dasu banda Husna itama Ummy saida tabata go ahead tai kawa da ita sannan tayi.

Babban akwatinta taciro daga wardrobe tabude batamasan metake packing ba, duk abinda hannunta yakai kwasa kawai take, saida akwatin ya cika sannan tarufe, tahada textbooks nata duka a school bag nata tarataya abaya sai dayan akwatin taja tabude kofa tafito tanaja da kyar sabida carpet na hana akwatin tafiya, ga nauyin na makaranta kuma dake shoulder nata, dago kai Abba yayi ya kalleta dake zaune a falo strictly yace “dakata” tsayawa tayi kanta akasa, Abba yataho ya hayo benen har inda

take yana zuwa wajen hannunsa yakai kan kafadanta ya karbi jakan saiya daura a saman akwatin sai yadauka yafara tafiya a natse yace “let’s go” yanda yadaga akwatin bazaka dauka ya kwana biyu a duniya ba yashiga sauka benen Ahlan na binsa a baya ahankali har kofa yafiya yajuyo ya kalleta, ahankali tafito itama ta tsaya gefensa saitaga yaciro key yana rufe flat din hawaye taji sun zubo mata dasauri takai bayan hannunta ta share fuskanta tajuyar da kanta tana kallon compound din exactly yanda yaran dake shakkan mahaifinsu keyi, Abba yaja akwatin bayan yagama rufe flat din, dasauri security yazo wajen harda gudunsa yace “Sir I can get this for you” anatse Abba yace “barshi nagode Abbakar, let’s go Ahlan” yayi magana da Ahlan dake gefensa hakan yasa tafara tafiya shima Abba haka suka wuce har flat na farko, da kansa yasa hannu yabude kofan yashiga da sallama, wasu manyan hamshakan mata ne zaune a falon kan kujera suna kallo suna hira sai yan matan dazu sunacin abinci a dinning, sai maza biyu manya dan zasuyi 30something, duk sukabi Abba da kallo ganinsa ya kinkimo akwati da kansa, dasauri Babban namijin yatashi yataho yace “Abba lemme help with that” ahankali Abba ya sakin masa yace “kai sama Abdullahi” yajuyo yakalli Ahlan dake bayansa jikin kofa kanta akasa bata shigoba tana wasa da hannunta hannunsa yasa yakama hannunta datake wasa dashi yace “shigo ciki” yasa dayan hannu yarufe kofan sanna yasaketa yace “wuce dinning kici abinci tare da yan uwanki” gyadamai kai tayi ahankali sannan tafara tafiya tazo gaban matan kanta akasa taduka tace “ina yini Hajiya, ina Yini Adda” daya daga cikinsu tace “lafiya lau Ahlan an dawo daga makaranta, to maza jekici abinci” dagowa tayi saita juyo takalli Yayansu dake zaune yana kallonta tace “ina yini Ya Bello” yana kallonta yace “how are you Ahlan”? Ahankali tace “fine” saita mike tsaye tajuya tawuce dinning jikinta duk yayi sanyi kana ganinta kaga hakan, Abba yabita da idanu karaf akan idanun Matansa Adda wacce itace matarsa tabiyu bayan uwargida wacce suke kira da Hajiya, tadaure ta danne duk abinda takeji tace “Alhaji lafiya muka ganka da Ahlan this night yarda sai anyi da gaske ake ganinta ware haka banda safiya damuke samin ina kwana da kyar” karasawa Abba yayi yazauna a natse daidai Ya Abdul dayakai akwatinta sama na saukowa yana gyara hannun rigansa, Abba ya kalli Uwargidansa dake kallonsa itama yadanyi gyaran murya yace “narabu da mahaifiyar Ahlan!” Kowa na dakin saida ya kalli Abba banda Ahlan dake zaune a dinning tana juya spoon acikin abincin dake gabanta, da mamaki kowa yake kallon Abba sabida yanda Abba keson Kutub itace yar gaban goshinsa, babu wanda yace wani abu dan zancen ne yazo musu wani bagatatan kaman saukan aradu, Abba yace “aurena da ita yakare due to wasu dalilai daba huruminku bane kusani tsakanina ne da ita wannan” yadanyi shiru saiya kara kallon Hajiya yace “ga y’ata Ahlan bazan barta ita kadai tai rayuwa a flat dincan ba, tana bukatan iyaye mata dazasu sa idanu akanta, saisa nakawo miki ita kirikemin ita, idan bazakiyi ba tell me yanzu sabida nasamo mai kulamin da ita, I’m not forcing you idan kince no I will understand you” dakin tsit yayi ko karan numfashi bakaji, this is just Abba very authoritative mutum ne, baida wasa, kafiyayen murdadden mutum ne shi, matansa basa iya ja dashi ko kadan kowa shakkan sa yake, daga yaran har matan, dudda magananan yama Hajiya zafi sosai amman tadaure ta danne tai murmushin yake tace “Ahlan ai diyata ce, su Ramla daman sun dawo wajena duk saisu zauna tare, Allah yamusu albarka” Abba yakalli mazan yace “kusa idanu akan kanninku mata Abdul, ban yarda diyata ta kula maza a waje ba this has always been my rule, wanda yamiki magana ku aikosa wajena, zanyi bincike idan bai kwanta min ba, nida kaina zan nema muku mazajen na aurar daku kaman yanda nama yayyinku, am I clear Rahma, Maryam and you Ahlan”? Yayi maganan yana kallon dinning, atare Maryam da Rahma sukace “eh Abba” Ahlan takasa magana sabida kuka daya cika bakinta yana gab da yazubo jin Abba ya sanar da cewa yarabu da Ummy, Abba ya tsareta da idanu jin bata amsa ba, Rahma ta tabata tace “Abba na magana dake Ahlan”dan juyo da kanta Ahlan tayi kadan idanunta sai kyallin hawaye suke muryanta was sounding kaman tana mura sabida kuka tace “toh Abba” dauke kai Abba yayi saiya kalli su Rahma dake yace “ga yar uwanku, kanwarku ce, kuhada kanku, banson fada hayaniya ko tsokana ku kiyaye

now that her Mom is not here keep her company” atare sukace toh Abba, dan kallon Ahlan yasakeyi yakalli abincin datake wasa dashi bataciba har yanzu yace “finish that food kafin nadawo daga sallan isha’i Ahlan” gyadamai Abba kai tayi Abba yamike mazan ma suka tashi suka fice zuwa masallaci.

Kaman jira Adda take Abba yafita tawani buga uwar shewa tana dariya tace “wai balarabiya naji ana cewa an saka an kora bata gidan nan Yaya”? Hajiya tace “nima haka naji” zokaga dariya, suma yan matan suka kwashe da dariya, Adda ta dakatar da dariyan tace “ohh Allah kenan yanzu duk tsiyan da Matar nan ta shuka agidan nan ana mana yanga an haifi yarinya yar fara mai gashin larabawa yanzu yar ce anan an kawo mana mu murike” Hajiya tace “gakota nan kina gani flesh and blood aban tausayi” Adda tawani mike tsaye tana kama waist ta kalli dinning din tace “ke zonan dan ubanki” kan Ahlan na kasa ko motsi batayiba Rahma tawani hankadeta saida tafadi kasa tace “bakiji Mamana nakiranki bane shegiya” fashewa da kuka Ahlan tayi sosai daman tuntuni take rike kukan, azuciye Adda tazo wajen tawani fizgo Ahlan tace “uban me kikema kuka yanzu dukanki akayi kome eh ke adole shagwababbiya, koko so kike ki rabamu da mijin namu musan dake zamu fara kishi tunda uwarki bata nan eh”? Girgizamata kai Ahlan tayi jikinta na rawa sosai, Adda tace “to dan ubanki yimana shiru kamin namiki na jaki shegiya makira, hadiye kukan” hadiye kukan Ahlan tayi gabanta na bala’in faduwa tsoron su take bana wasa ba, Adda zata kara magana Hajiya tace “kinga yana nan barta haka”.
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 8
Shigowa falon Hajiya tayi idanunta sunyi jajir tasami Mamanta har lokacin kuka take Hajiya na lallasjinta idanunta sunyi jajir, ganin yanda mamanta ke kuka kawai tafashe da kuka itama Adda ta taso dasauri tana goge hawayenta tazo wajen kawai Ramla tafada jikinta Mommy “Mommy zan mutu, Mommy zan mutu, wlh bazan taba taba yafewa Ahlan ba, Mom idan ban auri Ya Habeeb ba zan mutu wallahi tallahi” Adda tace “bazaki mutuba Ramla” Hajiya tace “abin sam ba dadi baimin dadi ba amman kiyakuri Ramla kidena cewa zaki mutu” sakin Ramla Adda tayi tana vibrating tace “Hajiya Ahlan, Ahlan” sai kawai tasaki Ramla tai stairs da sauri Hajiya tabita tace “ke Adda me zaki, Maman Ramla, Maman Ramla, mutumin nan fa na gidan nan eh“ bude kofan dakinsu Ahlan Mom tayi dakin duhu ba haske ta kunna wuta, Ahlan na kwance kan gado tarufe da bargo fuskanta a bude tayi nisa a bacci haka Maryam ma wani zuciya ne yadauki Adda kawai tadauki pillow daga gadon Ramla tahau kan ruwan cikin Ahlan tadaura akan fuskan Ahlan ta danne da duka karfinta na duniya tana ihu tace “kimutu kowa yahuta, ki mutu” daidai Hajiya da Ramla na shigowa dakin, Ahlan tafara shure shure Hajiya tarugo da gudun gaske tanajan Adda tace “ke Zainab, Zainab, Maman Ramla kin haukace ne zaki kasheta fa” itama Ramla tazo dagudu tanajan Mamanta tace “Momm Mommy please Mom stop, Mommy tashi akanta, Abba na gidan nan don’t put us in trouble” bude idanu Maryam tayi jin hayaniya sosai, Adda kaman ta haukace tace “wallahi saina kasheta akaini gidan yari na tsani yarinyar nan” ihu Maryam tayi “Mommy zata mutu” Hajiya tace “Maman Ramla kin haukace ne stop this nace zata mutu fa” wani kalan shure shure Ahlan takeyi na rashin numfashi ganin kafafunta na neman dena motsi da duka karfinta da kibanta Hajiya tasa ta hankada Adda, Mommy tafadi akasa tana dakama Adda tsawa tace “Yanda kika tsani yarinyar nan nina fiki tsananta amman kisan kai daukan ran dan Adam is never the solution are you mad”? Dasauri Maryam tacire filon Ahlan nawani irin nishi fuskanta yayi jajir Hajiya tajuya takalleta ta bala’in tsorata batasan sanda dakanta takama Ahlan tana jijigawa tace “na shiga uku na lalace, Innalillahi wa innailahi raji’un zata mutu, ke karki mutu a hannuna na shiga uku, bani ruwa maza Maryam bata numfashi ta sankare” da gudun gaske Ramla tai bayi kafin ma Maryam taje tadauki bowl ta kampato ruwa tafito takawo Hajiya ta karba ta kwarama Ahlan tundaga ka wani kalan nishi tayi numfashinta nadawowa.
□AUREN HADI□

✍M SHAKUR

EPISODE 19
Sannan ta iya fara kokarin bude idanunta tana wani jan numfashi Ramla, Maryam da Hajiya dukansu suna kanta suka shiga fiffitata Ahlan tabude idanunta tana dawowa daidai jikinta nawani kalan kyarma bata taba ganin mutuwa ido da ido ba sai yau Mommy ta taso wani girrrrrr jikin Ahlan yafara vibrating, Mommy tanunata da hannu tace “kika kwacema diyata miji is just step dakika taka da ni Zainab bazan taba kyaleki ba nahakura, uwarki tamin nayi hakuri, amman kima diyata wallahi sai inda karfina yakare, saina halakaki Ahlan! Sainaga bayanki a wannan dogon kasan Ahlan! Saina kasheki wallahi! Daga yanzu duk sanda kika ganni ki chanza hanya dan saina zaman miki annoba wallahi! Idan kuma an haifeki kin haifu ki sanar da ubanki ko uwarki abinda namiki kowani mahaluki, wallahi saina azabatar dake! Sainasa maza goma sun miki fyade sun nakasaki har abada! Shegiya tsinanniya! Wannan faran fatan da nonuwan da gashin dakike mana alfahari dashi saina sa an watsa miki acid kin damaji for life! Ni da ke muxuba this is just example watch out for me Ahlan dan kin tsokano devil zan iya hakura akamin but not my children, I will hunt you Ahlan!” Adda na maganan tajuya tafita Ramla tabita da sauri, Hajiya tasaki Ahlan yarinyar tadan bata tausayi sabida hatta hanjin cikinta kadawa suke bawai tanason Ahlan bane amman taji wani abu kawai tadauke kai tace “ki zauna da ita Maryam” tawuce itama tafita daga dakin Maryam tazo wajen tazauna tana kallon Ahlan da jikinta kewani irin rawa bamata hayyacinta tsabaragen tsoro ahankali Maryam tace “kice la’ilaha illallah Muhammadu Rasulullah….” Motsi Ahlan tafarayi da bakinta da kyar tasami tafara furtawa ita kadai tasa ya zuciyanta yamata tana cikin bacci fa taji an danne hancinta da fuskanta gabaki daya batasan ina kanta yake ba wani tsoro taji all kalaman da Mom tagaya mata na dawo mata azuciya takai awa daya ahaka take, metama Ramla? Wani miji? What was Mommy saying? Maryam ma hankainta yakasa kwanciya bata gane kan maganan ba, tace “ina zuwa” tawuce tafita daga dakin, kofa Ahlan take kallo gani take kaman Adda zata dawo wayanta tashiga lalube bamata ga wayan ba takasa dauke idanunta daga kofan gani take Mom zata dawo, kankame jikinta tayi sai lokacin kuka yazo mata tafashe dawani irin kuka muryanta dabaya fita sosai tace “Ummy, Ummy, Ummyyyyy” bata tabajin tsoro arayuwanta kalan wanda takeji yauba, har asuba tana zaune awajen bata runtsa ko kulle idanunta ba, Abba yazo yayi knocking kofan alamun salla takasa tashi sabida tsoro saida gari yayi haske sosai Maryam tabude kofa tashigo dakin Ahlan ta kalleta ko kallonta Maryam batayi ba, bawai ta tsani Ahlan bane but Mahaifiyarta da Yayarta sun kwana suna kuka all because Ahlan ta kwacema Ramla Habeeb, tafi kowa sanin yanda Ramla keson Habeeb, mazan dasukace sunason Ramla a university nasu sunfi biyar amman bata taba kulasu ba sabida tasan Habeeb akace zata aura, kawai gani tayi kula Ahlan kaman she’s betraying her own sister ne,
Kawai tasan bazata taba bari Mamanta ko Ramla su cutar da Ahlan ba, Ko kallon Ahlan batayiba tabude wardrobe tadauki kayan dazata saka tawuce tafita ko kallonta batayiba, jikin Ahlan yakara sanyi takara tsorata takasa motsi fa.

Har 8 Abba yaji shiru bata fito ba sai kawai da kansa yamike yawuce stairs yayi knocking gaban dakin nasu saiya bude kofan ahankali wani kalan firgita tayi ta kalli kofan dasauri tsareta da idanu Abba yayi yace “ba makaranta ne yau?” Bakinta tashiga budewa tace “a…ak….akwai…..” Abba dake kallonta yace “tashi kije kiyi wanka” gyadama Abba kai tayi tamike ahankali Abba yajuya zai fita atsorace tace “Abba” takira sunansa da karfi abinda bata taba yiba, juyowa Abba yayi ya kalleta, baki tabude zatai magana saita fashe da kuka tace “Abba tsoro nakeji” Abba yakalleta yace “tsoro, tsoron me”?Tuna maganganun da Mom tamata jiya tayi, bayan hannunta takai tana share fuskanta tace “akwai cockroach abayin Abba please kajirani nai wanka” sosai Abba ke kallonta she looks really scared, saiya wuce da kansa ya kunna wutan bayin nasu ya shiga da kansa yana dube dube ko cockroach daya bai gani ba, saiya fito yace “jekiyi wankan” gyadamai kai tayi tajuya ahankali tashiga bayin Abba yabita da kallo juyowa tayi ta kallesa ganin still yana cikin dakin

tsabagen tsoro bata gama rufe kofan bayin ba tabar kadan abude Abba ya kalleta saiyabi dakin da kallo baiga Ramla da Maryam ba yadan sauke ijiyan zuciya, kwashe yaranta tayi tabar Ahlan tadinga kwana ita kadai ko me? Abba ya tambayi kansa, ita kanta Ahlan bata taba sani zata iya shiga wanka tabude bayi kadan Abba na daki sabida tsoro ba, ko kallon wajen bayin Abba baiyiba but he stood a tsakiyan dakin harta gama wankan tafito daure da towel Abba ya kalleta yace “maza shirya kifito ina jiranki a falo, yajuya yafita”

Kaya taciro dasauri abaya tasaka tahau kan dadduma tafara salla subconsciously tana juyowa dazaran taji wani motsi tsabagen tsoro tana sallamewa tamike tadauki jakanta, wayan ma mancewa tayi tadauka daga kan gado tafito nose mask shima mancewa tayi, Abba na zaune afalo ya tsareta da idanu something happened jiya, something is wrong tana zuwa yanuna mata abinci yace “ci” duk yanda taso taci abincin takasa tea tasha kadan tace “cikina ke ciwo Abba” mikewa Abba yayi yace “muje” fitowa compound sukayi ga mamakinta Mom tagani a compound din tsaye tareda Gardner dinsu tanamai maganan flowers tawani juyo takalli Ahlan da idanunta dasuka ji farin kwalli kuma sunyi jajir, kawai Ahlan taji tai baya Abba yariketa yace “watch ur step” bata kara gigin kallon wajenba har sukakai mota suka shiga, akaja motan, saida suka shiga hanya Abba yakalleta yace “wani abu yafaru jiya da daddare?” Girgizamai kai tayi, yace “toh why are you so scared today?” Ahankali tace “cockroach dana gani ne” Abba bai kara magana ba chan yace “I know Mamanki bata gidan nan but if you have any problem zaki iya gayamin, mamakin batanan but ina nan kuma kinada gata, no body can bully you na barsa, Maman su Ramla tace miki wani abune”? Dawani kalan sauri Ahlan tace “a’a bata gayamin komiba” Abba yatasateta da idanu bai kara magana ba har sukakai hospital.

Saukowa tayi daga motan tawuce ciki direct A&E dasauri tawuce dakin da aka kwantar da Ummy danta gayama Ummy harda gudunta tana zuwa tabude dakin chak ta tsaya sabida babu wanda tagani adakin, an gyara dakin ma, wucewa tayi bayin dakin tabude bakowa ciki, tafito dasauri daidai ana bude dakin Dr Ashraf ne yakalli gadon saikuma ya kalli Ahlan kai tsaye yace “ina Ummy”? Murya chan kasa tace “banganta ba” tsareta da idanu yayi yace “what happened to your face? Did you sleep at all”? Gyadamai kai tayi tana sauke kanta kasa tana wasa da yatsunta, wani babban Dr ne yabude kofan yashigo yace “Dr Ashraf naga shigowan ka ne saisa nabiyoka the patient tasa an sallameta last night” dasauri Ahlan tadago kanta takalli Dr dake magana, Dr Ashraf yace “what do you mean you discharge her she’s not fit to be discharged? And baka sanar dani ba when I brought her in” Dr yace “babu abinda ban fada mata ba tahanani kiranka na sanar dakai,
She even sign discharge against medical advice form, she used the hospital phone and get a uber wai she lost her phone, ta tafi she’s going back home she gave me this to give her daughter I guess kece yarta naga kaman ku” yayi maganan yana kallon Ahlan data kasa motsi yabata letter hannu Ahlan tasa ta karba, Dr yace “tace na maka godiya she gave me this to give you” yaba Ashraf wata yar karaman takarda, Dr yace “bari naje”warware takardan Ashraf yayi Ummy tarubuta “thank you Dr Ashraf, please take care of Ahlan for me I know you’re a good man” warware latter Ahlan tayi tafara karantawa tace “_My Noori I don’t want to tell you goodbye akan idanunki I know you will cry for me banson hakan, you said something jiya akan mesa muke boye miki abu ke ba yarinya bace, I thought of it, and you’re right, My Noori is 20yrs, a whole adult, I think I’m ready to tell you abinda yasa Abbanki yasakeni, back in yamen nataba aure when I was 15yrs, na auri wani gang leader haka, bamu haihu tareba, he’s into trafficking yara da drugs bayan ya mutu sojoji sun harbesa akace dole nice yarubuta as next of king nacigaba da business din, rayuwana ya fara chanzawa when I met Babanki i genuinely loved Babanki tunda har na iya barin kasata nadawo Nigeria sabida shi, still dana dawo nan nacigaba da running empire na, but bayan na haifeki naji I want to stop, I want out, gradually nafara denawa na

sanar dasu nadena they were not happy, shine suka nemi Babanki and told him everything da evidence, Babanki yasake ni, but nasan ba hakanan ne yasakeni ba, I'm sure yasakeni ne sabida yana tsoro yacigaa da zama dani mutanen zasu iya blowing whistle su fadi gashi gashi hakan can affect election dinsa, I was so angry daya sake harna masa alkawari i will take revenge menene menene but bayan mutanen sun kamani cus sun biyoni Nigeria nai tunani I was wrong, inason Babanki banson anything yasamesa ko yashiga wani matsala sabida ni, idan bana duniya babu wanda na yarda yana sonki tsakani da Allah kaman mahaifinki Ahlan, mutanen sun kwace wayata da komi harda passport, by the time u are reading this nasan cewa nariga nakai embassy yamen anan Abuja, I will turn myself in and expose komi dana sani kan empire sabida ayi shitting operation din down, zasuyi deporting dina to garin mu, I will go to prison pay for my crimes idan harna fito I will come back to you kinji y'ata, koda 100yrs yadaukeni I will come back to you Ahlan, what I want from you is kicigaba da karatu kidage become a doctor and leave a very happy and fruitful live, I'm sorry inada bad past bad history I'm sorry Mamanki was once a criminal I did lot of bad things, I watch girls masu shekarunki ana saidasu ana turasu kasahe daban daban sune suna karuwanci, wasu ana maidasu delivery agent na drugs, inacin kudin inajin dadi, Ahlan Ummy ki is a bad person saisa Babanki ya saketa, yakuma ki fada miki cus bayason ki tsanani, bayason kiyi rayuwa kina tunanin so this is my Mom this is abinda tayi, I'm sorry Ahlan, I love you so much, I'm so sorry for everything be happy okay, be happy my Baby girl, Allah yamiki albarka, Allah ya karemin ke, I love you alot Ahlan Noor!" Ummy_

Wani kalan numfashi Ahlan taji saita dunkule letter a hannunta kawai gani tayi dakin na juyamata, motsi tayi zatai tafiya kaman ance Dr Ashraf yajuyo kawai yaga zata fadi dawani kalan sauri yatareta tafado akan kirjinsa a sume letter na faduwa kasa.
□AUREN HADI□

✍M SHAKUR

EPISODE 20
Chak Dr Ashraf yadagata yadauketa yana daurata akan gadon yana danna wani botun saiga Doctor guda biyu da nurse daya sun shigo nurse din tashiga warware mata veil na kanta Ashraf yakama hannunta ahankali da kansa yanemi line yamata fixing drip, yaduka ahankali yadauki letter yayi jmmm saiya shiga folding letter yakawo ya ijiye kusa da ita ya tsaya akanta yayi folding hannunsa a kirji yay shiru yana kallonta sauran doctors suka shiga dubata har suka gama.

Ya lumshe idanu thank god today is off day nasa, zama yayi akan kujeran wajen yana zaune har 1 yafita yaje yayi salla yadawo yasake zama yayi folding hannunsa a kirji yana kallonta la'asar tayi yawuce mosque yana fitowa yashiga mota wani eatry yaje yasayo abinci da juice yadawo dakin drip din yakare yacire yasake zama around 5 tashiga bude idanunta kafin takarasa bude idanun tasss tadaura akan saman dakin tana kallon sama komi nadawo mata when did her life change from white to blue, hawaye ne ya gangaro ta gefen idanunta yana sauka zuwa kunnenta ahankali Ashraf yace "hey!" Dan juyo da fuskanta tayi tadaura rinannun idanunta akan fuskansa yana mata wani kallo cikeda so yace "I'm right here, I will never ever leave you alone kinji Ahlan" tsaresa da idanu tayi yau kawai takasa daurewa tafashe dawani kalan kuka tana kallonsa sosai, tsareta yayi da idanu yana ganin yanda take kuka yanajin everything a zuciyansa kaman yasata ajikinsa ya lallasheta, baice mata komiba yabari tai kukan mai kyau duk tana kallonsa har saida ta dakatar da kukan, yazaro handkerchief mai kyau yabata karba tayi ahankali takai kan fuskanta ta share tasss,

ahankali yace “okay first thing first tashi kizauna and have something” girgixamai kai tayi Ashraf yace “no tashi tashi” ahankali ta tashi jin kanta abude dasauri ta daura hannayenta saman kanta cikeda kunya, dauke kai yayi yashiga bude abincin yace “gyalenki nakusa dake is the nurse that open ur head dakika suma” dasauri tajuya tadauki gyalenta tayafa akanta tana mammaida gashinta ciki takalli letter dake kusada ita dasauri tasa hannu tadauka ta tura kasan filo dan batason kowa yagani shima yayi kaman bai ganiba yajuyo yabata abinci wani lafiyayen fried rice ne da chicken yabata, hannu tasa ahankali ta karba da spoon idanunta akasa asanyaye tace “thank you” abincin ta deba kadan takai bakinta da kyar ta hadiye bakinta badadi kaman yagane, cold watermelon juice yamika mata tadan kallesa murmushi yamata wani sanyi taji, tasa hannu ta karba takai baki ta kurba tasauke hannu yabata basa tayi ahankali tana sauke idanunta kasa takara deban rice din takai baki, da kyar taci quarter abincin ta ijiye a gefe, juice din yabata ta shanye, wani kalan tausayi take basa kuma yana balain jinta aransa he knows she going through a lot agida dudda baisan menene ba exactly, ahankali tace “thank you” gyadamata kai yayi yace “stand up you need to pray zansa nurse tazo tacire miki kanula din, bari nadanje waje ko” gyadamai kai tayi, wucewa yayi yafita tabisa da kallo hakanan yana fita saitaji komi yadawo mata sabo kaman presence dinsa narage mata wani damuwan letter tadauka tasaka a jakanta saita wuce bayi tayo alwala dadduma ta shinfida tafara salla azahar da la’asar nurse tazo shigo tace “sannu” ciremata tayi tanadan yatsine fuska
Knocking Ashraf yayi yashigo rike dawani karamin bag, nurse tace bari naje, jakan yabata yace “don’t cry today okay, if you cry my heart will tell me” yanuna mata zuciyansa, sauke kanta kasa tayi akunyace, tawuce tafita.

Fitowa ahankali take tafiya gabaki daya batada karfi still yauma Abba ne yazo daukanta bude mata motan akayi tashigo magana yake a waya more like meeting ma, zama tayi bata iya ta gaidashi ba cus maganan seems serious ahaka har sukakai gida lokacin magrib, kawai ana bude gate na gidansu taji kirjinta na bugawa dum dum dum kaman zai fita, akai parking kasa motsi tai saida Abba yadanna wayan yasaka a mute yakalleta yace “shiga gida kiyi salla and eat nima masallaci zan shiga” gyadamai kai tai sannan tasauko daga motan ahankali tashiga tafiya zuwa flat din kaman bataso taje saida takai gaban dakin ta tsaya cha takasa bude kofan tashiga saida taga Abba na saukowa daga motan sannan tai maza tabude kofan tashiga da Mom idanunta suka fara haduwa dake zaune kan doguwan kujera, Hajiya zaune kusada ita, ga Ramla zaune kusada Mamanta tadaura kanta akan cinyan Mom idanunta sun kumbura ga magunguna gefensu kaman Ramla batada lafiya, Maryam dake zaune a dinning da laptop agabanta tana kallo a Netflix kowa kallonta yake babu murmushi akan ko fuskan mutum daya kasa motsi tayi jikinta yahau rawa sabida tsoro batasan sanda tajuya tabude kofan tafita ba dasauri Mom tace “tsinanna ai da kin shigo dan kutumar uwarki” Maryam kawai tadauke kai tacigaba da kallonta, jin zuciyanta yakasa daurewa sai kawai ta tashi tadauki laptop dinta tawuce sama gwarama bata gani ba, Ahlan tana fitowa Abba yariga yatafi mosque, tsayawa tayi gaban dakin takai kusan 20min jira take ko Abba zai shigo ya shiga da ita amman shiru har wajajen 8 nadare, bude kofan falon akayi aka fito Mom ce, wani kalan komawa baya Ahlan tayi har tana faduwa ta tashi tsaye da sauri kaman taga mala’ikan mutuwa kawai tajuya tai garden dinsu na gidan da sauri Mom tai wani makirin murmushi tawuce flat dinta abinta tabude kofa tashiga.

Har wajajen 10 goma nadare Ahlan na garden dinsu tsaye sauro na cizonta, tana zaune akan plastic chair kawai taji muryan Mom tace “Ke!” Dago kanta tayi tahada idanu da Mom dake tsaye jikin katuwan bisiyan garden dinsu na mango this time tana sanye da wata faran doguwan gown ga bakin kwalli a idanunta kaman aljana

tanama Ahlan wani kallo kaman zata kasheta baki Ahlan tabude zatai ihu sabida yanda ta mugun tsorata, Mom tadaura hannunta kan lips hakan yasa tarike da hannu Mom tamata alamu datazo rawa jikin Ahlan yashigayi tana kakkarwa tashiga tahowa saida tazo dab da ita Mom tawani fizgota takama kanta cikeda asalin tsana tabuga ajikin bishiyan saiga jini nabin gefen fuskanta ta kasa ihu ko magana sabida wani irin tsoron Mom, Mom ta matseta jikin bishiya sosai ta daura hannuna a kirjinta ta danne taciro wata karaman wuka tana kaiwa wuyanta tace “kin dauka wasa nake jiya danace zan kasheki”? Wani bahaggon numfashi Ahlan kawai take, Mom takawo fuskata dab dana Ahlan dake numfashi da kyar tace “Wallahi Wallahi saina kasheki Ahlan kafin rannan daurin auren nan! Wallahi saina kasheki! Na rantse da Allah kafin nan da sati biyu saina kasheki, Habeeb na Ramla ne!” Mom ta matseta ko numfashi bata iyayi, cikin wani irin murya tace “duk randa kika bude baki kika kira sunana kan namiki wani abu zaki ganni a inda bazaki taba tunani zaki ganni ba kaman yanzu and you can never ever hide from me ko cikin uwarki kika koma I will find you and eat you bakisan waye ni ba” saitadan koma baya tabar kirjin Ahlan ganin zata mutu takai wukan kasan wuyanta tace “nabude kofan garden dinnan dazai kaiki waje ta dayan layin, leave this house karki kara dawowa har abada only that can save you from dying, kika fara gudu karki tsaya inba hakaba zaki ganni koda akabari kika boye, wuce kitafi kafin na kirga uku” tawani tunkuda Ahlan akasa tai wani mugun faduwa jikinta na rawa Ahlan tamike tai wajen kofan tana waigen Mom data biyota tafita ta kofan tana fita taga maza wasu gardawa su biyar suka kwashe da dariya sukace “gata nan tazo, kai kuma zatai dadi, ku dauketa muje bayan gari” wani kalan gudu Ahlan tafara ta manta da goshinta dake jini, layinsu ba mutane kusan duka layin ma gidan Babanta ne gudu kawai take tana waigen baya mazan na Binta dan kwalin yafadi ahaka har suka fita daga bayan anguwansu gudu take, sai mazan sunkai wajen mutane sai suyi kaaman ba binta suke ba.

Wani kalan gudu Ahlan take Ummy ta kawai take tunani batamasan a ina take ba, tai gudun da tunda take bata tabayin kalan sa ba, wlh tayi gudu yakai na 30min straight, tana gudu kan wani hanya tafadama wani keke da sabida yaci mugun birki yasa baiyi mugun kwasheta ba dan electric bicycle ne batama hayyacinta kawai tacigaba da gudu tana waigen baya tafada wani anguwa da kaman sabin estate da ake ginawa ne duk empty houses ne uncompleted, dan juyawa yayi yabita da kallo yadan yatsine fuska yacigaba da tuka keken ahankali kawai saiyaga maza su 5 irin mazan dakana ganin kasan thugs ne suna tafiya sai yajuyar da kansa yakalli baya yaga baiga yarinyar ba probably tafada one of those uncompleted houses wucewa yayi yacigaba da tuka kekensa jikinsa na fadamasa wani abu kaman this guys yarinyar chan sukebi, ta madubi yaga mazan sun kwasa da gudu suma kawai saiya tsaya chak yana kallon madubin ganin sunyi cikin wajen gidajen hakanan kawai saiyayi kwana da keken sa cikin wani kalan zuciya kaman Superman ya tsaya gaban wajen saiya sauka daga keken yayi parking yashiga tahowa yana tafiya kaman zaki saiya duka karsu gansa yashiga tafiya, ihun mace yaji saikuma yaji shiru dawani kalan sauri yashiga uncompleted building dayaji sound din, babu haske sosai banda hasken wata but yana iya ganinsu sun yagama Ahlan hannun abayanta sun tura material din abakinta takasa ihu, an kwantar da ita akasa maza biyu sun rike hannuwanta ga daya ya tsaya a samanta yana kwance belt din wando yana shan wiwi da hannun daya, da kafa daya dake cikin sport canvas nasa Habeeb yasa yadaki wani katako dake wajen ya karya pass yadauki rabi yarike a hannunsa hakan yasa duka mazan suka juyo suka kallesa, cikin wata kalan murya that is black dark muryan cikaken namiji kaman soja yace “you have 10seconds, I mean seconds guda goma tak ku sake ta ko you will regret crossing part with me!”.
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 21
Ba karamin firgita sukayi ba ganin wani yabiyosu, dudda Ogansu ya firgita amman cikin fushi yakalli Habeeb dabaya ganin fuskansa sosai yace “ina ruwanka Malam? Me ruwanka damu? Matata ce kabar nan k…….” Cikeda tsantsan rashin imani da tausayi Habeeb yadaga katako nan yakaimai a kumatu batare dayabarsa yakarasa maganan ba dan 10seconds yacika, ayanda katakon yasauka gefen fuskan Ogan saida ya juyar da kansa gabaki daya hakoran dake cikin bakinsa guda hudu saida suka fita kawai yay wani tangal tangal yana layi yanaso yayi magana ma yakasa kawai yafadi yazube wajen a sume, sauran boy guys din arude sukace “Oga, kai Lado, Oga Lado” biyun dasuka rike Ahlan dake ihu da baya fitowa suka dagata suka jata zasu wuce dayan kofan da ita su fita, jefo katakon Habeeb yayi yachaki hannun daya daga cikinsu daya rike hannun Ahlan dashi, wani irin zaro idanu Ahlan tayi ta sankare awajen gayen na ihun azaba, cikin wani kalan zuciya yama biyun dake gabansa wani kalan bakin duka na total nakasa mutum, sannan yakaraso yana wani kalan tafiya kaman boss, kirjin Ahlan wani irin bugawa yake, bata taba ganin mutum mai karfi haka ba gashi babba, yashiga tahowa wajen kawai kallonsa Ahlan take trying kozataga fuskansa da kyau amman bata gani, hakan yasa wanda yake wajen yasaki hannunta dasauri zai gudu kawai Habeeb yasa masa kafa ya fizgosa yajuyo dashi kawai yadaukesa yadagasa sama gabaki daya Ahlan tai wani baya tace “wayyooo! Zai mutu kasakeshi ahaka, he might be brain dead or be left with spinal cord injury, I’m a Doctor” Ahlan tai maganan abibbirkice, still Habeeb na tsaye yadaga guy din sama har lokaci yana kallon fuskan wacce ke maganan da jikinta is literally shaking, yadan tabe baki yace “do I care”? Kawai yasaki guy din yanda kan Ahlan yajuya ganin abinda bata taba ganiba kawai tai luuuuuu tataho zata zube ta gaba a sume zata fadi Habeeb yadan tsaya saikuma yadanyi karamin tsaki yasa hannu yatarota, fadowa Ahlan tayi jikinsa, ko kallon fuskanta baiyiba yakai dayan hannunsa yataba aljihunsa tana jikinsa, yacire wayansa yay dialing number Ibrahim, yana dagawa yace “I’ve sent you wani location can kazo wajen yanzu, also come with police, be fast I have somewhere to be” yana maganan ya katse wayan ya ijiye akasa yakalli fuskan Ahlan da baya wani gani da kyau sabida ba haske yakalli hannun riganta dayake abude ga bra strap dinta kana gani that is loose, dauke kai yayi yasa hannu yazare exercise jacket din dake jikinsa na nike yadaura mata ajiki yarufe ta, daidai Motan Ibrahim na parking yafito dasauri yashigo wajen yana daga murya yace “Habeeb, Habeeb” Habeeb yadaga murya yace “over here” dasauri Ibdahim yabi muryansa yana yafito da wayansa ya kunna flash yataho wajen ya tsaya yana ganin kattin maza dasuke akasa ga jini ko’ina ga Habeeb duke rike da wata dake jikinsa but bai tabata ba, yataho dasauri yana haska fuskan Ahlan yace “what happened”? Batare da Habeeb ya kalli fuskan Ahlan ba yace “where are the police”? Ibrahim yace “gasunan zuwa natura musu location din ni I was close by daman zan koma gida ne naga location din saisa nazo what happened”? Ahankali Habeeb ya mike ya kwantar da Ahlan akasa batare daya kallate ba yace “take this girl to the hospital let her get checked, I’m off to my circling workout I’m late” kawai yayi waje Ibrahim yace “are you for real to wa zai bada statement”? Habeeb dake tafiya abinsa yace “gaka”yawuce wajen electric keken sa yahau yawuce dadai police na isowa Ibrahim yabada statement na rape yadauki Ahlan yawuce da ita hospital wani private some police biye da shi, sharp sharp aka karbeta sai kallonta yake kaman yasanta amma yarasa a ina yasanta.
□AUREN HADI□

✍M SHAKUR

EPISODE 22

Wuraren 10 nadare Abba yashigo gidan tareda Bello da Ya Abdullahi tsaresa akai dawani meeting a masallaci, yau awajen Adda yake amman sabida Ahlan yawuce flat din Hajiya sabida ganin dayayi yau su Ramla basu kwana dakin ba, she might be scared with the whole cockroach drama datamai yau, bude kofan flat din yayi yashigo bakowa a falo probably kowa yaje ya kwanta, sama yawuce agaban dakin yaran ya tsaya hannu yakai yay knocking ya dakata, shiru babu wanda ya amsa, maybe sunyi bacci, bude kofan yayi ahankali yanakai hannu ya kunna wutan dakin amman baiga kowa adakin ba, sake bin dakin yayi da kallo akaro na biyu ko school bag dinta bai gani ba, bayin dakin ya kalla saiya wuce dasauri this time around bai ma tsaya knocking ba bude kofan bayin yayi, baiga kowa cikin bathroom dinba, dasauri yafito daga dakin yanakiran sunan Ahlan da karfi, “Ahlan, Ahlan, Ahlan, Noor!” Yana maganan yawuce wajen dakin Hajiya data shiga bude kofa tana fitowa jin muryan Alhaji tace “lafiya Alhaji kake ihu da daddaren nan?” Kai tsaye yace “ina Ahlan?” Dan tsayawa tayi tace “Ahlan? Dazu muna falo tashigo tana ganinmu tajuya tafita ba uhmm balle gaisuwa, bata cemana wani abu ba”Cikin tsananin fushi Alhaji yace “what do you mean tana ganinku tajuya?” Cikin dan fushi dan Hajiya tasoma gajiya da lamarin Alhaji tace “you just asked question nabaka amsa, tana lekowa tajuya tafita without saying a word binta zanyi sabida yar yaye ce ita koko rarrafe take? Ni banda yanzu ma dakake nemanta nadauka tashiga daki damuka wuce sama muyi salla” cikin tsanain fushi Abba yace “well she’s not here ko’ina yarinyar nan tashiga ku nemota inba hakaba you will see the other side of me wallahi Nafeesa” Abba yakira sunan Hajiya direct yajuya ya shiga sauka daga bene Hajiya tabiyosa hankalinta yadan soma tashi sabida batason any abu dazai hanata zama First Lady of Nigeria idan sukaci zabe, compound Abba yafito cikin fushi yace “security, security, Bello, Abdullahi” yawuce flat din Adda yana bubbuga kofansu, Ya Bello duk suka fito daga flat nasu da gudu securities naziwa suma da gudunsu, Adda tabude kofa Ramla da Maryam biye da ita, yanda taga fuskan Abba saida ta girgiza amman tadake tace “lafiya Alhaji kake bugamin kofa haka this night kasan inada BP”? Wani kallon suspect Abba yake mata cikin kakkausan murya yace “ina Ahlan?” Cikin fada Mom tace “kaman ya ina Ahlan? Adakina Ahlan ke zama koni kaba amananta? Kawai zakaz……” “for the last time ina Ahlan nace?” Abba yadakama Mom tsawa da kowa saida ya girgiza awajen itama tadake tace “bansani ba” Abba yayi shiru yana mata wani kallo Mom tace “I don’t understand bakaga yar gwal dinka and kazo kana tashina daga bacci kanamin wani kallo what do you mean? You think I will hurt yarka? Mesa da banyi ba sai yanzu eh? Bari kaji Alhaji I can’t hurt a fly talk more of a human”, kadakai kawai Abba yayi yajuya saikuma yajuyo yakalli Mom sosai yanunata da yatsa yace “idan i ever find out you have anything to do with rashin ganin Ahlan da ba’ayiba wallahi it will cost you aure na dake, I can forgive you idan you hurt me Zainab, amman i can’t forgive wanda zai taba Ahlan” Abba yajuya dan ya zuciya yau ba kadan ba, compound dinsa gabaki daya babu CCTV camera awaje kawai yazagaye da cameras, yakalli su Abdallah da securities yace “search everywhere and every corner of this house for Ahlan” kowa yace yes sir.

Duk aka juya Mom dasu Ramla da Maryam duk na tsaye da Hajiya, kowa ya tsorata ganin yanayin Abba, ita kanta Mom tace tsorata amman tadake, daga garden Abdallah yace “Abba Abba”Dawani sauri harda gudu gudu Abba yawuce wajen su Hajiya da Adda da yaran suka dibi jiki suka bi bayansa, school bag na Ahlan Abdullahi yanunamai yace “Abba this is her school bag, everything is intact” Bello dake wajen kofan garden din yace “Abba this door is open, probably tanan tafita” Adda tace “za’amin sheri yarka tanachan tabar gida halan ma wajen wani saurayinta ta……”Zainab! Abba yadaka mata tsawa yace “leave this place immediately!” Juyawa

Adda tayi azuciye fuuuu tawuce Abba yatako zuwa wajen kofan saiya bude ahankali da kansa ya kalla ko'ina interlock ne abunka da area masu kudi babu wani footsteps kowani abu, kirjin Abba kawai bugawa yake yadan fuzar da iska ahankali yace "Alhahuma Ajirni fi musibati" yashiga tafiya yake chan da dan nesa saiya tsaya yaciro wayansa, number Excellency yaciro yayi dialing ringing daya yadaga yace "Alhaji Muhammadu" anatse Abba yace "na'am Excellency, ammm akwai wata yar matsala Excellency."
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 23
Cikeda natsuwa Excellency yace "what happened Alai Muhammadu"? Dan ijiyan zuciya Abba yasauke yace "Ahlan tabace!" Dasauri Excellency yace "Ahlan? Ahlan dakabar office zuwa daukota a clinic? A school ko asibiti tabace kome?" Ahankali Abba yace "ni mundawo I dropped her at home nawuce nafita zuwa magrib an rikeni a mosque I just got back nace bara nadubata before sleeping she's nowhere to be found, munga school bag nata a garden, kofan garden is open that means she use the door tafita saisa none of the security guards sukaga sanda tafita"gently Excellency yace "do you think she run away?" Ahankali Abba yace "no Ahlan ba irin yaran nan bane, batada any reason na guduwa" Excellency yace "did you involve the police?" Ahankali yace "no kaina fara kira, I know police means press su sani yazama another different news da headlines" Excellency yace "good just stay put I'm coming over there now I know wani top private investigator I'm calling him now, don't worry we will find Ahlan"Excellency yace "kota gudu neman Mamanta ne?" Abba ya girgiza kai yace "no that's not Ahlan, something is happening in this home that I don't know yet, mata are complicated this morning she was so scared saida na tsaya na jirata tai wanka, I am 100 percent sure dasa hannun matana aciki but I have nothing to prove that" Excellency yace "gani nashiga mota I am coming just stay put" dan ijiyan zuciya Abba yayi yace "tom Allah kawoka lafiya Excellency" yacire wayan daga kunnensa Ya Abdullah yafara zuwa wajen yace "Abba yaya za'ayi?" Anatse yace "bari Excellency ya iso tukunna" sai kowa yakoma ya tsaya Abba ya bala'in damu, mezai gayama Kutub? That's the question dakemai yawo a zuciya.

Dayake duk abarayin masu kudi suke within 20min Excellency ya iso daidai ana budemai mota wayansa yashiga ringing, saukowa yayi Abba nataho wa wajen, Excellency yaciro wayansa daga aljihu yana kallon screen din dan ya dauka investigator daya kirane sai yaga Ibrahim, ba kasafai Ibrahim ke kiransa ba hannu yadagama Abba alamun ina zuwa yasa wayan a kunnensa yace "Ibrahima" anatse Ibrahim yace "Baba I'm together da yan sanda they want me to follow them to police station" dasauri Excellency yace "akanme? Meya hadaka da yan sanda? You forgot abinda nace no police with election around the corner" dasauri Ibrahim yace "eh nasani Abba saisa nakiraka daman" Abba yace "what happened?" Ibrahim yace "amm Baba daman Habeeb ne zai tafi circling workout dinsa so he met some thugs trying to rape wata yarinya he saved her and call me ina zuwa yabanni da ita yace nakira police shi sauri yake, yanzu muna hospital an kwantar da yarinyar police wants me to go with them nabada statement" the only thing dayayi ringing akan Excellency is Ahlan dasauri yace "kace a girl wace girl?" Ibrahim yace "koda nazo she's uncoucious Baba bamusan sunanta ko anything ba" Excellency yace "can you snap her ka turomin hotonta" dasauri Ibrahim yace "no she's with doctors" Excellency yace "okay stay where you are send me location na hospital din, I will make few calls on my way coming karka cema police din anything" Ibrahim yace

“okay” Excellency yakatse wayan kawai yakama hannun Abba yace “let’s go I have a feeling Ahlan ce” Abba yace “mene” Excellebcy yace “I will tell you a mota” dasauri Ya Ibrahim da Bello suka biyosu duk suka shiga mota ga motan escort gabansu aka jasu while Excellency nafadama Abba komi.

Another 20min suka bata daya kaisu asibitin suna shiga sukaga Ibrham tareda yan sandan daidai baban likita mace nazuwa kafin Abba yayi magana Excellency yace “likita i will love to see the patient I think diyata ce” likita tace “sure Sir” saita juya Excellency da Abba suka bita bude kofan dakin tayi chak Abba ya tsaya ganin Ahlan kan gado an yakamata hannun Riga ga jacket na Habeeb ajikinta har lokacin kanta abude gashinta duk kasa hakama hannunta ga bandage a gosinta Excellency ne ya iya karasawa gaban gadon ya tsaya su Ibrahim kuma ganin yanda Abba ya tsaya yakasa shiga ciki sai Ibrahim da Bello da Ya Abdullahi suka taho wajen, ahankali Excellency yace “Innalillahi, wat did you find out Dr” Dr tace “luckily koma waye ya ceceta he saved her on time bata sami any kind or form of internal abuse ba, kanta ne yafashe as u can see inda nasaka bandage sai kuma bruises a hannunta da kafafunta which duka munyi treating mun mata alluran tetanus she just needs rest, kubarta tahuta zuwa safiya sai asallameta” Excellency yace “thank you nagode nagode likita, ngode, Ibrahim get money from the car this Dr personally give her 5millon da SUV, share the rest of the money to all the staff of the hospital Abdullah kuje kutayasa” zubawa Dr tayi gaban Excellency tace “Nagode, Nagode ranka shi dade, wayyo Allah na SUV am I dreaming, Allah yakara daraja Alhaji” Excellency yace “dainamin godiya bakisan me kikamin ba for saving this my daughter” Dr ta tashi tafita still tana godiya, Excellency ya kalli Abba da damuwa ke kan fuskansa yace “tahonan” anatse Abba yataho ya tsaya gaban Excellency yana sauke ijiyan zuciya, Excellency yace “akwai wanda kabawa katin bikin nan ne?” Girgiza kai Abba yayi yace “no just family na nuna mawa jiya” Excellecy yace “good cus idan this girl continues staying there in that house something will happen to her, gobe Juma’a ko”? Abba ya gyada masa kai, Excellency yace “zamu maida daurin auren nan jibi rannan asabar, za’ayi reprinting invitation card din this night tommorow we share it dakowa, and tommorow we make the official announcement” Abba ya gyadamai kai, Excellency yayi shiru yace “daganan zan zata koma gidan Mairo Sister Umma su Habeeb tazauna da ita for just tommorow zuwa Saturday, she’s not going back to your house, bari naje nai magana da yan sanda I need them to investigate those 5guys da akai arresting”Excellency yawuce yafita Abba ya tsaya gaban gadon yana kallon Ahlan yakai hannunsa ahankali yadaura kan bandage dake gosinta yayi shiru. “Maisa mata are wicked? From yanda yarinyar nan ta tsorata takasa wanka saida yazo dakin he knew it has something to do with matayen sa, somehow yafi zargin Adda baya zargin Hajiya, Hajiya da batada hayaniya ma hade kan dasukayi da Adda yamaidata gabaki daya wani kala” kauda tunanin yayi bayason zargi, dukowa yayi ahankali ya manna mata kiss a goshi yana kallon jacket na jikinta idanunsa suka sauka kan karfen zip na jacket din da aka rubuta Habeeb ajiki dan customize sport jacket ne from Nike, shiru Abba yayi, could Habeeb and Ahlan be destined together? Cus mesa shine Allah yatura ya ceceta? Habeeb baisan Ahlan ba, maybe ko yasan Ahlan lokacin she might be around that kind 3, 4, 5yrs, for Ahlan batasan Habeeb ba at all, first of all Mamanta bata cika zuwa gidan excellency ba cus she always feels batada spot a gidan dan already matan excellency da Hajiya da Adda suke shiri sosai, so inba gaisuwa ko occasion ba babu abinda ke kai Kutub gidan saisa Ahlan bata cika zuwa gidan ba, su Ramla sune yan gidan sunsan ciki da waje na gidan wajen zuwa su ne every now and then, he knows Habeeb is stubborn ada yana tsoro but with what happened today sai yaji kaman sign Allah ke basa na karya kara damuwa dan Habeeb da Ahlan are destined to be together.

Dawowa ciki Excellency yayi rikeda wata waya yace “this is the text message da yan sanda suka samu daga wajen Ogan yan ta’adan” ahankali Abba yasa hannu ya asma yana karantawa. “_wata matashiya nakeso kumata fyade maza dayawa kuka gama kuje ku yardata wani wajen, ga addressing inda zakuzo ku tsaya gaban kofan kudu daga wajajen isha’i duk wacce kukaga tafito itace yarinyar, zan bada miliyan daya advance idan aikin yazama successfully zan biyaku da kyau_”
Dago kai Abba yayi yakalli Excellency, Excellency yace “this proves my suspicions right is from your home so Ahlan tagama zama dasu, the police are working on gano number waye zasuyi tracking number” anatse Abba yace “Maman su Ramla nake zargi”Excellency yayi shiru yace “koma itane mezakayi? Kash aurenku zakayi? You have daughters da ita, sometimes mata are very stupid basuda basira, my advice is ai Ahlan ce problem din ko toh bazasu kara ganinta ba, she’s leaving the house just ignore her kabarta tunda yanzu zargi ne, and Alhamdulillah Ahlan is safe, but idan takara trying any nonsense kadauki mataki tattsaura but yanzu kabarta da halinta ko itace koba ita bace kai koma waye” gyadamai Excellency kai yayi, Excellency yace “nakira Mairo na aika deiver na yaje ya daukota she will be here, zata zauna da ita sai muje mu kwanta we will have a long day gobe da jibi”Abba ya gaydamai kai, duk suka cigaba da tsayuwa chan saiga Ibrahim yabude dakin yashigo tareda wata yar dattijuwa kamilan gaske da Hijabi ajikinta dudda kana ganinta kasan Excellency ya girmeta amman cikeda girmamawa yace “Adda Mairo yakuri natashe ki da daddaren nan” murmushi tayi tace “bakomi ai d’a nakowa ne, Ahlan kuma ai tazama diyata tunda matar dan Yayata zata zama dudda baida kirki Alameen”dasauri Abba yace “ina yini Hajja Mairo” murmushi tayi tace “Muhammadu Ya iyali yakuma Ahlan to Allah ya kiyaye gaba Allah ya tsare, kutafi kuje ku kwanta babu abinda zai faru I will be here in sha Allah”Excellency yace “zanbar direba incase kinason wani abu zaki iya aikasa, Babanta zai hada kayanta ya aika zuwa gidanki” Maito tace “toh toh shikenan bakomi saida safenku” Abba yace “Nagode Allah saka da alkhairi” Mairo tace “kaga sauda sagenku kudenamin godiyan nan” suka wuce suka fita, duk mota suka shiga Excellnxy yasauke Abba da su Ya Bello awaje, sannan yayi sallama Abba yace “Nagode Nagode Excellency” Excellency yace “Muhammadu kaga duk abinda yasameka fa niya sama good or bad, kasan it has always been like this tun kafin mukawo matakin nan damuke ayau, so kadenamin godiya, me and you together we will do good and we will make Nigeria a better country sabida munada zuciya mai kyau da izinin Allah, go get some rest gobe zamu sanarwa da duniya zancen auren yaranmu, this is the last big step na nunama jama’an Nigeria finally sun sami mutane masu amana dazasu shugabanci kasan nan” Abba ya gyadamasa kai yace “mu kwana lafiya Excellency” yajuya yashiga gida bodyguard yarufe ma Excellency motan yawuce yashiga, Ibrahim dayake cikin motan dan motansa aka barwa Mama Mairo a hospital da driver guda daya yace “Baba daman wannan ce yarinyar da zaka aurama Habeeb? Daman da gaske kake”? Excellency yay yar dariyan manya yace “eh itace Ahlan duk baku santa sosai ba mahaifiyarta lokacin bata cika zuwa gidan mu ba sauran matan dasu Ramla sukafi zuwa”Ibrahim yace “eh su Ramla da Maryam ai yan gidane, but I know Mamanta wannan balarabiyan koda Umma tarasu she was there, no wonder danaga yarinyar nadinga tunanin kaman na santa awani waje” Excellency yace “zamu daura musu aure jibi rannan asabar I’m sha Allah!”
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 24
Shiru Ibrahim yayi danshi kansa baitaba dauka da gaske Baba yakeba sai yau yadauka kawai yana maganan ne sabida Habeeb yashiga taitayinsa, Excellency yadan sauke ijiyan zuciya yace “I have a task for you Ibrahima” dasauri Ibrahim yace

“wani task Baba”? Dan murmushi Excellenjcy yayi na manya yace “kaida babban mutumin Habeeb, task dinka is ka kawomin Habeeb central mosque wajen daurin aurensa koda ko zaka kullesa ne do whatever it takes”shiru Ibrahim yayi yama kasama Baba magana, Excellency kawai yasake murmushi yasan bakaramin aiki yaba Ibrahim ba, ahaka suka kawo gidan around 12 nadare daidai ana parking shima Habeeb yashigo gidan da keken yana uban zufa yayi workout Excellency yasauko daga mota ya tsaya yana binsa da kallo Habeeb yawucesu ko kallon inda suke baiyiba yana zufa Ibrahim ma ya kallesa, yana zuwa parking keken yayi yasauka rigace kaman singlet ta workout jikinsa na Nike, muscles dinsa saika tsorata ka kalla, yana sanye dawani gajeren wando da canvas yasaka sock yajuya yashiga tafiya yana dumfaran flat din Ammi, Excellency kawai kallonsa yake har saida yashiga ciki, Ibrahim yace “saida safe Baba” Excellency yace “good night Son” wucewa Ibrahim yayi zuwa flat dinsa dan ya kwanta yabar yar matansa mai karamin ciki, Excellency yadade tsaye yana kallon gaban flat din Ammi tun rannan daya karbi passport dinsa saiyau yake kara sasa a idanu kuma ko gaishesa Habeeb baiyiba, ba flat din Ammi yake ba yana bangaren Hajiya Asabe Uwargida all this while taje Umara ne dazun nan da daddaren nan tadawo baima hadu da ita ba kawai yawuce flat dinta.

Ammi tayi bacci koda yashiga flat din, maida kofan yayi yarufe yawuce wajen fridge yabude yadauki bottle water yabude yana sha tafiya yaji hakan yasa yadago kansa, Ya Sadiya yagani kallo daya yamata yadauke kai yacigaba da shan ruwansa zuwa wajen tayi ta tsaya tana kallonsa ijiye bottle din daya shanye tass yayi yazo yawuceta baice mata uppan ba zai fara hawa staircase ahankali tace “Alameen!” Chak ya tsaya saiya cigaba kuma da tafiya, cikin wani kalan murya dake rawa sosai tace “Habeeb I’m sorry nasan abinda muka maka muna yan uwanka bamu kyauta ba, kome kake we should stand by you Habeeb not opposite of that, I’m sorry” cigaba da tafiya Habeeb yayi abinsa, wani kuka taji yazo mata muryanta narawa sosai tace “look at me yanzu, sabida abinda namaka Allah is punishing me too, this is the 6th year danai aure ko barin wata bantabayi ba balle nasa ran zantaba haihuwa, and I know duk alhakinka ne kebina!” Chak Habeeb ya tsaya jin maganan datayi, Ya Sadiya tafashe da kuka sosai, rashin haihuwa na damunta shine biggest matsalanta arayuwa, cikin wani kalan kuka tace “I’m sorry Habeeb, I’m sorryyyyy” har cikin ransa yaji yanda take kukan, juyowa yayi ahankali yadaura idanunsa akanta ta girmi Habeeb fa but yanda yadauki kansa you will think shine yayanta amman itace yayan tabasa 2yrs, ahankali yashiga saukowa daga staircase din yana dawowa saida yasauko gabaki daya ya tsaya gaban benen yana kallonta fuskansa ba yabo ba fallasa yana kallon yanda take kukan her body is shaking yace “rashin haihuwanki have nothing to do with abinda yasameni, karki kara blaming kanki!” Yafadi maganan cikin husky voice nasa ya tsareta da idanu she’s still crying, yakai almost 1min yakasa tafiya yakasa cemata tayakuri, ahankali yace “can you stop crying”? Ahankali Ya Sadiya ta gyadamai kai, juyawa yayi zai fara hawa bene kawai saitazo da gudu tai hugging nasa ta baya, tsayawa yayi chak tasake fashewa da kuka tana shesheka tace “I love you so much Habeeb, wallahi I love you alot, I’m sorry kaji, I’m sorry for hurting you” kawai jikinsa yayi sanyi yakai 1min ahaka gently saiya juyo, hugging nasa tayi a kirji, ahankali yadaga hannusa saiya daura akan bayanta tareda lumshe idanu yana sauke ijiyan zuciya murya chan kasa yace “stop crying please banson kuka Ya Sadiya” murmushi tayi murya chan kasa tace “I know my little brother baison kuka tun muna yara, idan kaga ina kuka zaka iya bani duka snacks dinka dan naitaci nadena kuka, and tun kana yaro you hardly cry, ni da Ya Jay can cry amman kaida

kake karami idanunka kaman an kona basu da ruwa” dago fuskanta yayi daga kirjinsa saiyakai hannunsa yashare mata fuskan yayi wiping tears din murmushi tayi sosai, strictly yace “is ur husband maltreating you sabida rashin haihuwa?” Dan dariya kadan tayi tace “a’a Yaya Habeeb kafin kaje ka kakkaryamini dan mijina” still basawa kan fuskansa yace “then why have you been here tunda nazo you’ve been in this house? Ina yake”? Ahankali tace “tafiya yayi yaje Russia for wani course but he’s coming back next week Friday” gyadamata kai yayi yace “I have wani friend he’s a Doctor a UK he helps couple masu neman babies, idan mijinki yadawo talk to him sai kuje UK ku gansa yadubaku, zaki haihu okayy” gyadamai kai Ya Sadiya tayi tana murmushi tace “my brother is back Alhamdulillah, nabika dakinka muyi hira? Zan baka labarin every everything daya faru”? Ahankali yace “sure” atare suka wuce sama har dakinsa tana jikinsa, Ammi da kukan Sadya yasa ta farka she head everything tace “Alhamdulillah Alhamdulillah Alhamdulillah, Allah na godemaka, Ya Allah ka kara hada kansu”.
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 25
Wuraren 6 nasafe Ahlan tashiga bude idanunta kadan kadan kafin takarasa bude idanun gabaki daya tabi inda take da kallo wnada clearly tagane hospital ne, tajuyo da kanta wata mata tagani kan dadduma ga charbi a hannunta tanaja, yunkurowa tayi zata tashi zaune jikinta namata wani irin ciwo tai dan kara. “Ya Allah….” Juyowa Mama Mairo tayi dasauri ta mike ta taho wajen gadon tace “Ahlan kin farka, sannu taso” Ahlan takalleta dan batasan matanba, Mama Mairo tace “Bismillahi sannu sannu kinji” daidai ana bude kofa Dr nashigowa tace “you are awake, ya jikin? Meke miki ciwo yanzu”? Ahankali Ahlan tace “my head and body” daidai ana sake bude kofan da Sallama Abba ne yashigo dasauri Dr ta gaida Abba ya amsa yana karasowa gaban gadon, Dr tace “kikai wanka kici abinci kisha magani you will feel better here is discharge form naki you can go home” Abba yace “thank you Dr” yakalli Ahlan daduk tai wani iri yace “ya jikin” kanta akasa tace “dasauki” Abba yayi shiru Mama Mairo tace “bari tai salla kawa saimu tafi tayi wanka agida” anatse Abba yace “zan jiraku awaje saina kaiku dakaina” Mama Mairo tace “to shikenan” yajuya yafita yanda jikinta ke ciwo da ytaimaloj Mama Mairo tai alwala tafito hai kan dadduma magrib da ishai sai subhi duka tayi tama mamakin how did she end up in this hospital meya faru? Maisa Abb baice mata komiba dasaurab su, hijabi Mama Mairo takawo tasa mata tace “mutafi” Mama Mairo tadauki jacket din takama hannunta ahankali take taiga suka fito a reception sukaga Abba tsaye dasauri Ahlan tasake sauke kanta kasa waje suka fita suka shiga mota.

Sannan suka wuce har wani estate acikin Garki akai parking kofar gidan Abba bai shigaba yace “zan dawo anjima stay here Ahlan, all your thing na nan, bazakije school yau ba, rest Monday Kya cigaba, komi naki na nan including phone” gyadamai kai tai tayi Abba yajuya yawuce gidan nada kyau wlh and it’s big, wata yar matashiyane tabude kofa tafito dagudu tace “oyoyo Mama” takalli Ahlan tace “sannu Ahlan ya jikin? Sorry ko” kawai takama hannun Ahlan, Mama Mairo tace “Safiya bita ahankali” murmushi kadan Ahlan tamata suka shiga ciki gidan kamshin turaren wuta an gyara ko’ina, Mama tace “kaita daki taimakamata tai wanka bari nahada mata magani” Safiya tace “toh muje Ahlan” suka wuce sama, daki tabude mai kyau ga kayak Ahlan aciki Safiya tace “ga wayanki ma wata Hussy nata kiranki” Ahankali Ahlan tace “she’s my fried” zaunar da Ahlan tayi bakin gado tace “bari na kunna miki shower yayi zafi kafin ki shiga” tawuce bayi ta kunna tafito rike da towel mai kyau

tabata tace “bari naje nakawo miki shayi, tashi kishiga bayi”Ahankali Ahlan ta gyadamata ka tafita tashi tayi tashiga cire rigan tana kallon hannun daya yage saiya kalli jacket fake kan gado tasan na wanda ya taimaketa ne batasan waye ba but Allah ya biyasa, she was scared yesterday cus baby u wani naiji daya taba daura hannunsa akan jikinta da kafadanta sai jiya, rigan tacire tadaura towel tawuce bayi kanta yafi mata ciwo wanka tayi da ruwan zafi sosai tafito Mama Mairo tagani a dakin da tray ta ijiye akasa tace “yauwa bude drawer ki dauki kowani kaya kikeso kisa basai kin tsaya bude akwatin nan ba, saiki kari kisha magani ki kwanta, ajima Safiya saita tsefe miki wannan suman a wanke, gobe za’a gyarasa sai kuma ayi kunshi” gyadama Mama Mairo kai tayi ahankali tace “Nagode Mama” Murmusi Mama Mairo tayi tawuce tafita.

Gaban dressing mirror taje tashafa mai, saita bude wardrobe ne wani half gown tagani na cithen dake kamshin turaren wuta kawai tadauka tasaka tadawo tazauna tana daukan wayanta daidai Husna nakara kira ahankali Ahlan tace “hello Ahlan baganki jiyaba, bamuyi wayana nakiraki yafi sau goma, what happened?” Ahankali tace “banda lafiya ne, dasauri tace “subhanallahi meya faru?” Dan shiruuu Ahlan tayi, Husna tace “don’t worry idan muka tashi I will come nadubaki” ahankali tace “bana gidan mu” Husna tace “kina ina?” Dan shiru tayi sai ahankali tace “I will send you location” Husna tace “okay take care of yourself Allah kara sauki, I will bring ice cream for you kinji” Gyadamata kai tayi ta katse wayan tashi ijiye, shayin takalla saita kai bakinta Dr Ashraf ne yafado ranta kadan tasha saita ijiye takasa cin abincin, dakin tabi da kallo maganganun Mom nadawo mata kirjinta yashiga bugawa, bude kofan dakin Safiya tayi tashigo tace “laaaa bakici abinci ba” Ahlan tace “cikina na ciwo ne” Safiya tace “to ci waina ko guda daya ne da iya Ahlan taci sanna tabarta shigowan Safiya yasa taji tsoron datakeji yatafi chan sai ga Mama Mairo wani farfesun kaza takawo mata ta tsaya akanta taci bata wani dade daci ba sai bacci.

Aroubd 1:30 Husna tafito daga masallaci taga Dr Ashraf tsaye gaban mosque yana kallonta dan kunya taji tace “ina yini” batare daya amsaba yace “can I have Ahlan’s number”? Dan shiru Husna tayi tace “batada lafiyane saisa bata zoba” mikamata wayansa yayi, ahankali Husna ta karba saita bude wayanta ta kwashe number Ahlan tasaka masa tabasa karba yayi yace “thanks” yajuya kawai ya wuce tashi tsaya chak tabisa da kallo kawai yanzu abin yama clicking 100% Dr Ashraf dinnan son Ahlan yake, yanzu sabida Ahlan yabiyota har masallaci ya tsaya gaban kofan mata yana jiranta baiji kunyaba yabata wayansa tasa masa number Ahlan he’s seriously inlove with her.

Wuraren 3 wayan Ahlan yashiga kawo haske dan a vibration number yake amman tana bacci, Safiya dake mata tsufa ahankali ne takalli screen na wayan taga number ne ba suna, sabida dazu Ahlan tace mata tabata address na gidan nan Husna zatazo hakan yasa ta dauka Husna ne sai kawai tasa hannu tadauki wayan takai kunne tace “Hello Husna she’s sleeping” anutse Dr Ashraf yace “who are you?” Jin muryan namiji yasa gaban Safiya yafadi, ahankali tace “sunana Safiya”? Dan shiru yayi yace “yajikinta? Tasha magani”?

Safiya tace “eh tasha dazu da safe aka sallameta daga hospital yanzu she’s sleeping” Dasauri Ashraf yace “hospital?” Safiya tace “eh anan ta kwana kasan wasu maza sunso sumata fyad…..” Safiya tai shiru dasauri, ha’a ba gobe ne bikin Ahlan da Ya Habeeb ba, this man ba Ya Habeeb bane, waye shi yake kiranta jibi yanda takemai surutu, dawani kalan sauri tacire wayan daga kunnenta ta katse dasauri Dr Ashraf nasake kira ta katse kawai ta ijiye wayan kirjinta na bugawa tacigaba da mata tsifa.

Wuraren 4 Husna tai message Safiya tadauki wayan ganin is from Husna “Ahlan bazan iya zuwa ba akwai emergency a A&E wani bus tai accident a kawo lot of patients is all hands on head I will come gobe Saturday” ijiye wayan Safiya tayi, shima Ashraf bai sake kitaba sabida emergency surgeries from accident din.
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 26

Bangaren Dr Ashraf
Saida Dr Ashraf yayi da gaske sannan yasamu ya ijiye tunanin Ahlan a gefe and focus on lives na patient dake gabansa akan table, surgery yake back to back sai wajajen 8:15PM na dare finally yagama last surgery din, fitowa daga operation room din yayi ahankali, MD yagani awajen tana kallonsa dasauri yace “Mommy where you waiting for me ko kinzo observation ne?” Yayi magana yana wanke hannunsa yana cire komi na jikinsa na surgery” MD bata cemai komiba, yana gamawa kawai ta taho wajen hannunsa takama tace “come with me Ashraf” tashiga tafiya da sauri, binta Ashraf yayi cus tana rikeda hanunsa yace “Mommy, Mom, Hello Madam MD ina zaki kaini? I need to write report na surgery danayi kafin na manta abubuwan danayi” batacemai komiba, suna shiga office nata takalli secretary nata tace “no more visitors” dasauri secretary tace “yes Ma’am” MD tabude office nata tashiga still tana rikeda hanun Ashraf dayama fara dan damuwa ganin yanayinta, maida kofan tayi tarufe saita saki hannunsa ahankali tana kallon fuskansa wanda tana gani tasan baisan komiba saita wuce gaban table nata tadauki remote na tv dakin dake kan table tace “I remembered vividly kataba gayamin that girl dakakeso Babanta na neman president ko zai fito a mataimakin shugaban kasa?” Ashraf yataho yace “yes Mom meya faru? Something seems off with you” Mom ta tsaresa da idanu tama kasa magana sabida yanda kirjinta ke bugawa she’s extremely heartbroken for danta, dasauri Ashraf yace “menene Mom? Is something wrong?” Mom tace “sunanta Ahlan Muhammad ko? Dan I still remember name dakabani kace na sata a department naka” gyadama Mom kai Dr Ashraf yayi, Mom sai ta kunna tv dakin remote tace “watch this”talla akaje a channels television news sai gashi sun dawo mai bada news tace “kaman yanda muke fada kafin muje break, yau the entire nation witness something magnificent wato hada auren da presidential aspirants dinmu sukayi da yaransu sabida tabbatar mana da mu citizens na Nigeria unity da amana na cewa bazasu taba cutan amana mu, mu kalli video tare” sai gashi a nuno Excellency da Abba sun tsaya agaban mumbari na campaign ga uban mutane awajen suna warware wata takardan invitation card wanda camera yakara haskowa sunan Dr Ahlan Muhammad yakara flashing akan idanun Ashraf da kawai yadan girgiza idanunsa, ganin kaman idanunsa basa aiki baya gani da kyau, Excellency yace “you’re all invited to central mosque na nan Abuja gobe asabar karfe biyu dan sheda aure tsakanin dana Brr Alameen Habeeb dakuma diyar mataimakina Dr Ahlan Muhammad” motsi Ashraf yaso yayi dan gyara kafansa dayaji kaman bazai iya daukansa ba kawai sai yayi kissing balance zai fadi dasauri Mom tarikesa tace “Ashraf! Ashraf” ahankali yace “Mom can you give me water please”cikeda damuwa Mom tace “Toh Toh” dukawa yai kawai saiya zauna wajen, Mom takawo ruwan hannunsa yamika zaibama Mom kawai hannayensa biyun suka shiga rawa rawa kaman ansamai electricity, Mom tace “Innalillahi Ashraf!” Cikin wani kalan karfin hali still hanunsa na rawa muryansa ma haka yace “I…..I…am fine Mom….ban….bansan mesa jikina ke rawa haka ba….” Yakara kawo hannunsa Mom takai ruwan bakinsa bata samasa a hanu ba kurba yayi kadan yacire kansa yarike ruwan abaki yakasa hadiyewa ijiye ruwan Mom tayi idanunta sun kada sunyi ja,

batamasan mezata cema danta ba Ashraf irin mutanen nan ne da idan zasuso abu sunason abun genuinely da duka zuciyansh gabaki daya , kuma basa kallon wani abu inba wanna abun ba, kawai jawosa Mom tayi tasashi ajikinta ta rungume yay lamo a kirjinta Mom na shafa bayansa ahankali tace “kayi hakuri Allah zai baka wacce tafita, yaushe ne I was telling you zamanin nan ba’ason mace ayi zurfin ciki, iyaye can get her married to someone else” yadade ajikin Mom ahankali yace “Mom are you sure is not fake news?”Mom tama kasa magana kawai tai shiru tana bubbuga bayansa kankame maman’s a yayi cikin wata kalan murya dake rawa sosai tace “Mom ina zansa raina?, Mom I still have time before gobe karfe biyu I won’t give you, I love Ahlan itama tana sona I’m sure batasan da this arrange marriage ba, I have to do something” yafito daga jikin Mom, Mom tace “do what? Mezakayi few hours to aurenta?”

Tsayawa yayi wajen kofa yace “you don’t give you inhar soyayan gaskiya kake, I will fight for Ahlan till the end Mom” yana maganan yabude kofan office din yafice Mom tamike.
Wucewa yayi wajen dayayi parking motansa yashiga idanunsa sunyi jajir wayansa yadaga yayi dialing number Ahlan amman a kashe jefar da wayan yayi yadaura hannayensa biyu akan fuskansa yakai minti uku ahaka chan yasauke hannunsa yakai bayan hannunsa yana goge duka ruwan hawayen dake kan fuskansa idanunsa sunyi jajir ya fuzar da isa mai zafi yatada motan yaja har lokacin robe na asibiti ne ajikinsa blue, he knows gidansu Ahlan direct gidan yatafi tundaga nesa da gate din security suka taresa yayi parking yana sauke class security yace “wakake nema?” Yana kallonsa yace “Abba nazo nema Baban Ahlan” security yace “do you have appointment?” Ahankali Ashraf yace “no” security yace “he’s not back kodya dawo you can’t see him go back get appointment and go to his office anan ake ganinta he doesn’t entertain guest in his house” gyadamai kai kawai Ashraf yayi saiya juya yayi gaba chan kawai yayi parking, security yakalli motan sai kawai yajuya yakoma post dinsa Ashraf yacigaba da zama wajen ko tsakar dare Abba zai dawo he will wait for him anan, yana kallon hanya hawaye na taruwa akan idanunsa yanakai bayan hannu yana sharcewa da sauri.

WAYYOOO ASHRAF😭😭
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 27
Bangaren Ahlan
Wuraren 5 Ahlan ta farka she felt better sosai kan yadena ciwo, salla tayi Mama Mairo tazo takawo mata tsumi tace “sha wannan kifito masu gyaran gashi sunzo amiki” hannu tasa ta karba ahankali tace “nagode Mama” ta tashi batabi takan wayan taba anan kan gado tafice wayan ma mutuwa tayi dan ba’ayi charge nata ba, tafito.

House service ne kusan gabaki dayan saloon sukai setting up agidan, aka shiga mata gyaran gashin ba’abar ruwa yataba bandage na goshinta ba, akai amfani da abubuwa na kamshi aka gama aka turara mata gashin dake kamshi bana wasa ba around 7 suka tafi mai lalle zata zo gobe dasafe, Mama Mairo tace “kuje kuyi salla” dawowa sama sukayi yin salla, suna idarwa Safiya tafara fita ko 3min batayi da fitaba tadawo tace “Ahlan Abban ki yazo Mama tace akiraki, ki sauko kasa” tashi Ahlan tayi daga kan dadduma batare data cire hijabin dake jikinta ba tafito Safiya biye da ita amman saita wuce dakin Mama, Ahlan kadai ne tasauko kasa kanta akasa tana wasa

da fingers dinta Abba yabita da idanu hartazo wajen ta duka tace “ina yini Abba” batare daya amsaba yace “ya jikin akwai abinda ke miki ciwo?” Ahankali tace “no duk sun dena ciwo” Abba yayi shiru chan yace “meya faru jiya?” Dasauri ta kalli Abba lips dinta suka shiga rawa takasa hada karyan dazatayi yafito kuma kozataga mutu bazata kira suanan Adda ba, Abba ya jinjina kai yace “yayi kyau, take this” yamika mata invitation card din” ahankali tadago kanta saitakai hannunta ta karba tarike tana kallo Abba yace “bude ki karata” budewa tayi ahankali tafara karantawa the family of this this and ya sunan Abbanta invited you to the wedding Fatiha of their children ALAMEEN HABEEB & AHLAN NOOR MUHAMMAD wani dum! Dum! Dum! Dum! Zuciyanta yashiga bugawa ganin sunanta kodai gizo idanunta kemata Abba dake kallonta yace “na zaba miki miji Ahlan! Zan daura miki aure da dan excellency Alameen wanda aka fi kira da Habeeb!”

Wani gorrrrr kan Ahlan yayi kanta na ringing Habeeb da Adda tadinga mata mentioning kan ta kwacema Ramla miji tana cikin tunanin Abba yace “nasan it’s an Arrange marriage but it’s for the best, Habeeb yarone mai kirki infact shine mutumin daya taimakeki jiya daga hannun mutanen jiya” Abba yace “wannan auren gidane kinbar gida kin koma gida ne Ahlan dan both gidana da gidan Excellecy duk dayane, gobe daurin aure zaki tare dakin mijinki, za’a hada muku biki da walima daga baya, zancen school dazuwa clinic you will discuss it da mijinki, I know Mamanki batanan and step Mom dinki sai ahankali, ga Hajja Mairo ne tana matsayin Mamanki ne, Mijinki Habeeb kanwar late Mahaifiyarsa ce, zata miki duk wani abu dayakamata ama Amarya, zan dawo gobe na ganki kafin akaiki gidan Mijinki” wlh she feels dumb and numb duka at the same time wai kodai ba ita Ahlan dinba bata taba hararo za’a mata aure yanzu ba, she never ever see this coming with the way Ummy ta always take gayamata bata isa aure ba bata iya girki ba da sauransu, she can count how many times take gidan Excellency da wayonta baifi sau biyu zuwa uku ba batama san duka yan gidan ba bamatasan waye Habeeb dinba haka ake aure daman yadauka itane zata zabi miji wanda takeso ba ace an mata ba, kawai fuskan Dr Ashraf ne yayi flashing a face nata da yanda yagayamata yana sonta yacemata zaizo yaga Abba tahana sa how will he feel yazu yaji zatai aure ai kaman zata yaudaresa ne, tsareta da idanu Abba yayi bayan yamike ganin she’s lost, anatse yace “Ahlan look at me” dago idanunta tayi ta kalli Abba zata sauke idanunta kasa Abba yace “ba cewa nayi ki kalleni ba” gyadamasa Kai tayi, ahankali yace “you have anything to say? Idan kinada wata magana kiyi? Sannan you can object to marriage din” girgizama Abba kai tayi takasa magana tasauke kanta kasa tace “bakomi Abba” Abba yace “good dan ba option nake baki ba, make your marriage work, bakiyi nisa dani ba, auren gata namiki babu abinda zai sameki cikinsa, I wish you all the best in this new journey, Allah yamiki albarka, I will see you tomorrow” yana maganan Abba yamike yawuce yafita wani irin abu ne yatasoma Ahlan kaman amai dasauri ta tashi tai sama ta shiga dakinsu tabude bayi amai tayi tana wani irin nishi da kuka ansaki Ummy, Ummy commit crime yanzu haka maybe tana garinsu a prison, she met Dr Ashraf that is a good ma yace yana sonta yanzu zaiji tai aure ta yaudareshi yaya zaiji, then she’s about to get married to someone da bata saniba, idan wannan mutumin daya ceceta jiyane da gaske tayaya zatai rayuwa da mutumin da bada imani? Abubuwan da Mom suka fadamata nadawo mata bazata taba kyaleta ba tunda ta kwacema Ramla miji, batasan Habeeb ba amman she knows one thing tasha jin sunan Habeeb abakin Ramla most time a mota idan za’a dawo dasu daga school how will Ramla feel yanzu how will Ramla feel, wani kuka ne yazo mata zuciyanta namata zafi kawai tashiga rerawa kaman marainiya, she missed having Ummy ta, da Mamanta na nan tasan Ummy ta will stand did her she will talk to Abba amman yanzu batada kowa batada say how can she look at Abba and oppose abinda yace ko an samata wukaawuya bazata iyaba.

Wuraren 12 nadare Ashraf na zaune a motansa idanunsa sunyi jajir sundan taso abunka da faran fata, yaga mota na zuwa wanda yana ganin motan kawai yasan Abba ne aciki, bude motansa kawai yayi yafito baiyi wata wata ba yashiga tsakiyan titin kawai yayi kneeling securely na tahowa da gudu amman saida driver Abba yaci wani wawan birki Abba yace “lafiya Lawan” driver yace “wani ne yashigo titin yaduka gaban mota” Abba yadan leka daidai security kusan uku na zuwa sukace “Malam ko katashi ahanya Alhaji yawuce ko ranka yabaci” Ya Bello ne kadai tareda Abba hakan yasa yace “lemme check Abba” yasauka daga motan yataho wajen yace “what is happening?” Kafin suyi magana Ashraf yace “I’m not a criminal nazo nai magana da Abba ne, and I don’t plan on leaving this spot batare danai magan dashi ba saidai idan takeni motar zatayi da wuce” sake lekowa Abba dake taba wayansa yayi sai kawai yasauko Ya Bello na shirin magana saiga Abba anatse yace “what is going on here”? Yay maganan yana kallon Ashraf dake sanye da robe na likitoci dake kallonsa anatse Abba yace “tashi daga kasa amm Dr Ashraf” Abba yayi maganan yana kallon name din Ashraf that’s engrave a wajen pocket na gaban rigansa.
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 28
Ahankali Ashraf yatashi Abba yakalli securities yace “go back to your post” atare sukace “yes sir” duk suka juya suka wuce, Abba yakalli Ashraf yace “lafiya Dr? I don’t think I know this face? Meya faru kazo gidana nemana not office?” Dan ijiyan zuciya Ashraf yasauke idanunsa sunyi jaaa asanyaye yace “sunana Ashraf Aliyu I’m a Doctor a surgeon to be precise” yadanyi shiru both Abba da Ya Bello dake tsaye na kallonsa especially idanunsa dan yana magana suna kara taruwa da ruwa, kasa tsayuwa Ashraf yayi saiya kara kneeling agaban Abba gwanin ban tausayi yace “Abba ina matukar kaunar Ahlan! Zuciyata, raina, kuruwata gabaki daya beat for Ahlan, alfarma nazo rokonka karka hadata aure dawani, yau shekara hudu kenan inason Ahlan tundaga rannan farko da aka fara kawosu asibitin mu orientation and induction zuwa yau, ban gayamata ba sabida nabari tadan kara shekaru ne” yadan sauke ijiyan zuciya cikin wani kalan murya na wanda is disoriented yace “Abba kaji tausayina banda mahaifi dazai zo tayani fadamaka how much nakeson Ahlan, Babana ya rasu saisa nazo dakaina na tsareka cikin daren nan dudda nasan hakan baida kyau kuma bai dace ba, I’m so so so sorrry Abba” Wlh daga yanayin yanda maganan ke fita daga bakin Ashraf kasan he’s disoriented, sad, unhappy, scared, and afraid kai komima, tip na hancinsa ruwa ruwa shima na kuka, wani abu Abba yaji a zuciyansa Ashraf yabasa tausayi, d’a na kowane and kanason mutum baka fadi ba tsawon four years sai rannan dakagani a news is disheartening so koma menene humanity comes first da compassion cikeda tsananin mutuminci da karamma dan adam Abba yaduka yasa hannuwansa duka biyu yadaura akan kafadan Ashraf yace “tashi tashi denasa guiwanka akasa Dr” yakamosa ahankali Ashraf yamike tsaye gaban Abba kansa still yana kasa, Abba yakai hannunsa aljihu yaciro handkerchief nasa mai bala’in kyau da kansa yaduka ya share kasan dake knees na wandon Ashraf yace “jibi yada kasa kayanska sukai datti” kan Ashraf na kasa har lokacin, sake kallon fuskansa Abba yayi saiyadan sauke ijiyan zuciya yace “Ashraf from yanda kai magana dani I know kai yaro ne dake cikeda tarbiya dakuma sanin mutumcin magabantansa na yaba da hankalinka sosai” Abba yafadi ahankali sai yadan sauke ijiyan zuciya yace “maganan auran da Ahlan ba dazun ne fariyansa ba, nariga nabada aurenta ga Habeeb the only abinda yarage is gobe mutane su taru su shaida hakan” kawai fitowa hawaye yayi daga idanun Ashraf suka sauka akasa sabida kansa na kasa, Abba yadanyi jimm yace

“akwai wani abu daya danai imani dashi aduniyan nan duk wani abu idan naka ne dole zaka samesa whatever is meant for you is gonna be yours, kaman yanda hausawa ke cewa Matar mutum kabarinsa, Ashraf dattijo ne ni kuma dattijon kwarai mai alkawari da amana nariga nabada auren Ahlan I can’t go back on my word! Na tsaya ina maka bayanin man ne out of respect sabida mutuntani dakayi kai ka sanar dani bayan kaga news, kayakuri kaji Ashraf Allah ya kaddara ba matarka bace, amatsayina na mahaifin Ahlan ina maka fatan alkhairi sannan ina maka addua Allah ubangiji ya baka mata tagari kaji Allah yamaka albarka” Abba ya kalli Ya Bello yace “muje Bello”Abba yajuya zai wuce yashiga mota, Ashraf yace “Abba sabida political career dinka zaka aurar da Ahlan? Tanason wanda zaka aura mata? Wanda zaku auramata yana sonta? Idan Auren soyayya ne Ahlan na sonshi, shima yanason Ahlan zan rungume kaddara zan hakura, but I don’t think akwai hakan, this is just An ARRANGE MARRIAGE FOR POLITICAL ADVANTAGE, awannan zamanin damuke an daina yima yara AUREN HADI!” Shiru Abba yayi yana sauraronsa yadan sauke ijiyan zuciya saiya juyo yakalli Ashraf dayaga hawaye na sauka kan fuskansa yace “my family matter is a private abu, whatever decision na dauka akan yarana trust me bazan taba daukan wanda zai cutarda su ba, so once again Malam Ashraf I am sorry and ina maka fatan alkhairi!” Abba na maganan yajuya yashiga mota bodyguard nasa yarufe driver yaja motan Ashraf yabi motan da kallo saiya duka ahankali awajen Abba yana cikin motan amman yabisa da kallo ta madubi har saida suka shiga cikin gidan.

Securities sukazo wajen kai tsaye sukece .”Malam you have to leave before we report you to the police for being in our property” fuzar da iska Ashraf yayi saiya mike tsaye ahankali yawuce yashiga motansa ya kunna yabar wajen.
**

BANGAREN HABEEB!
Yau tun safe yafita yaje company shi he spent the entire day yana aiki meeting upon meeting wuraren 10 yabar office din yashiga motarsa yaja wayansa ne yashiga ringing ya kalla yaga Ammi ne yadaga kafin yayi magana tace “kana ina Habeeb”? Ahankali yace “gani a hanya ina dawowa” Ammi tace “okay drive safe” ahankali yace “okay Ammi” katse wayan yayi yashiga taba screen na motan dan kunna waka mistakenly yataba radio, dan tsuki yayi zai chanza daidai yakai wani intersectional bridge hakan yasa yamaida kansa kan titi daidai radio na cewa “jubilation all over Nigeria as the Nation favorite presidential aspirants announced the marriage of their children Barr Alameen Habeeb and Dr Ahlan muhammad that will happen tomorrow at national mosque Abuja at 2:00pm” wani mad break ya danna saida motan dake binsa ta daki bayan motansa horn aka shiga dannamai da sauri ya gangara gefen hanya yayi parking batare daya damu da damage da motansa tayi a baya.
□AUREN HADI□

✍M SHAKUR

EPISODE 29

□ Refresh Your Day with Hamy Green Tea □

Taste the blend that does more than quench thirst.
Hamy Green Tea = Premium Green Tea Leaves + Fresh Mint + Natural Spices

Benefits in every cup:
- Boosts energy & focus, no crash

- Soothes digestion with mint + spices
- Antioxidant-rich for that natural glow
- Clean, aromatic, and made in good condition

Proudly produced by:
Lukuku General Enterprises Ltd
Unit 1 Block D, M.O.W & Trans Technology Incubation Centre, Bauchi

Order/Distributorship: http://wa.me/08095660030
Follow us: IG @lukuku_enterprise | TikTok Lukuku General Enterprises Ltd

Sip healthy. Live fresh. Choose Hamy. ☕

He has been very busy today, is Baba seriously serious da yimai aure, babba dashi kawai Baba zai kama yamasa aure, bude wayansa yayi he knows he will see the news a punch news yaje da vanguard yaga gafa news baro baro saiya wuce instagram nan ne yaga proper video harda invitation card da Baba ke magan yana nunawa ransa yawani kalan baci ya kunna motan ya danna mata wuta sai gida dawani mahaukacin gudu yayi parking yana kallon motocin Baba haka yasa yadan yana nan fitowa yayi direct yawuce flat na Excellency yana zuwa gaban flat din ya tsaya sabida memories dasuka dawomai na mahaifiyarsa da randa Baba yakoresa acikin this same flat din same parlor, yakai 2 good minute yana tsaye kirjinsa na tafarfasa sai yasa hannu kawai yabude kofan yashiga ciki Excellency na zaune kan wata katafaren kujera one sitter yadaura kafafunsa kan wani karamin massage machine dake masa masa kafa ga glass aka idanunsa yana duba wani file yau ba hula kansa gashin kan duk furfura ga wata Hamshakiyan Hajiya agefensa zaune da fruits plate akan cinyanta tanaci ita tajuyo takalli Habeeb sabida ayanda yabude kofan shikuma Excellency ko dago kansa baiyiba cus he was expecting him daman abinda ke gabansa yake saima gyara glass din idanunsa dayayi yace “Hajjaju kinga kaman karfin gilashin nan yaragu” wani abu Habeeb yakaraji a kirjinsa bai rufe kofan ba yataho fuuuuu gaban Excellency ya tsaya da tsananin fushi zaiyi wani mugun fada saikuma yadanyi shiru uban furfuran daya gani a suman kan Baba, yadan lumshe idanu yana budewa yanaji kaman zai kama da wuta Hajiya Asabe tahada rai, da kyar kakkausan murya yace “I want to talk to you” batare da Excellency yakallesa ba yace “bakaga Mamanka ba baka iya gaisuwa ba Alameen” cikin fushi yace “Mamana tarasu” Hajiya Asabe taja tsaki murya kasa kasa tace “shashasha” wani juyo da kansa Habeeb yayi yamata wani kallo irin dani kike, mikewa tayi tace “Excellency bari naje sama saika shigo” tawuce tashiga hawa staircase abinta.

Habeeb yamaida idanunsa kan Excellency dake abinda ke gabansa takaici yasa yace “Baba I said I want to talk to you!” Chak Excellency ya tsaya shima Habeeb yayi shiru jin yakira Excellency da Baba is just slip of tongue, dan murmushi kadan Excellency yayi saiya rufe file din ya ijiye gefe yasauke kafafunsa dagakan massage machine din ya gyara zama yakalli Habeeb sosai yace “now that kayi realizing da Babanka kake magana you have my attention, ina jinka Alameen”zuciyan Habeeb tafarfasa yake sosai, yanuna tv da hannunsa yace “menake gani a TV? Just tell me bani Habeeb din kake cewa zakaiwa aure ba”? Cikin irin halin nan na iyaye dake nuna basa tsoronka ko shakkan ka ko tsoron masifanka Excellency yamike tsaye yace “ohh, ohh, i totally forgot, I save one card for you da kyar na samu wannan ya tsira na ijiye maka, duka sauran an kwashe an rabar, muyi printing about 5000 invitation card” Excellency yaciro katin daga aljihunsa yace “bari nacire maka daga envelope” yabude envelope din yaciro hadadden IV din yataho gaban Habeeb dake kallonsa sosai yakai hannunsa yakama hannun Habeeb yasamasa katin akai strictly yace “is not just news Alameen is real, aure zan maka, infact gobe ne daurin aurenka da Ahlan karfe biyu na rana!”Excellency yayi maganan yana kallon kwayan idanun Habeeb dasukai ja fuskan Babansa kawai Habeeb yake kallo yana huci Excellency dake kallonsa yace “ahaaa

ina jinka say something yaro na mai zuciya da taurin kai" akwai wani abu da Habeeb yakeji kaman zai mutu da ace wani ne ba Baba ba da wlh saiyamai shegen duka kawai kallon bakin ciki yakema Baba ba yanda zaiyi, Excellency yace "idan baka da abin cewa get out of my room I will see you tommorow at
central mosque" cikin fushi Habeeb yace "who do you think you are dazaka dinga juya rayuwata duk yanda kaga dama? Ka koreni daga gidannan 8yrs ago blaming me for mutuwan Umma, yanzu kuma ka kwacemin passport kahanani tafiya, still baka gamsu ba you went ahead kanamin aure, if you hate me this much maisa ka haifeni?" Habeeb yay ihu, Excellency yamai ihu yace "sabida ni ubanka ne!" Yadaki kirjinsa shima ba wasa yace "yes na koreka, kuma yanzu ni nace na mayar dakai, nina karbe passport dinka, ninace dole ka zauna gidan nan, sannan nine zan maka auren nan do you know why? Sabida I want to show you" Excellency yanuna kirjin Habeeb da yatsunsa yace "I want to show you nine ubanka! Habeeb I'm your father and dole kabi abinda nace sabida na isa dakai!" Dan matsowa dab da Excellency Habeeb yayi Excellency yace "yes it's okay the same way ka kashe mahaifiyarka nima kasheni yanzu kahuta!" Chak Habeeb ya tsaya idanunsa this time suka rikida suka koma baki kanana, gently yayi taking one step back yana kallon Excellency, kana ganin kallon dayakema Babansa kasan maganan ta tabasa sosai, cikin tsananin fushi Excellency yanunamai kofa yace "get out of my room Alameen kafin na sassaba maka" ko motsi Habeeb baiyiba kallonsa yake sai yadan sauke ijiyan zuciya kawai yajuya yayi tafiya one, two, three saiya tsaya saiya juyo yakalli Excellency yace "aurar dani zakayi go ahead and do it but I will tell you this" yanuna kansa yace "ni Habeeb bazan taba kaunar wacce ka zabamin a matsayin mata ba, I will never ever love her or have anything to do with her, sannan I will never accept her a matsayin matana, bazama kaganni wajen daurin auren ba so I will never consider kaina mijin aure ko mijin wata, indai nii zakama AUREN HADI kayi kuskuri Excellency!"Yana maganan yajuya Excellency yace "and I will tell you this for free Alameen, idan har nine ubanka na gaskiya saikaso yarinyar dazan aura maka sama da komi na duniyan nan damuke ciki! You will fall in love with Ahlan like a fool" ficewa Habeeb yayi yabugo kofan Excellency ya tsaya yana kallon kofan sai yayi murmushi kawai yana son Habeeb so na daban kuma shiya bata Habeeb, yasan Habeeb bai kashe mahaifiyarsa ba yakoresa ne sabida Habeeb ya gyara halinsa shine kuma yaba Ammi kudin databama Habeeb na tafiya yabar Nigeria, he make sure ya taimaki Hapeen ta karkashi in every step dayayi taking arayuwa bayan koransa daga gida, rannan dayaga Ahlan a school kwayan idanun Ahlan kadai yagani yaga akwai wani coolness a idanun yarinuar na Rahama dazai iya kwantar da zuciyan digadigan maza irinsu Habeeb, Ahlan yarinya ce mai tarbiya that's as pure as water shi yasan auren nan Akwai alkhairi yayi addua kuka akan hakan
Wucewa yayi abinsa yaje ya kwanta hankalina kwance yasa Habeeb will not accept the marraige but that does not mean zai cutar da Ahlan maybe yadaketa kowani abu no Habeeb is not like that.

Yanda yake tafarfasa yaso yaje flat din Ammi but baiso Ammi tagansa like that ko Ya Sadiya kawai siaya wuce wajen motansa yana tattaba aljihunsa yaciro kwalin taba yazaro kara daya ayanda yake fushi ya soyake yasha taban da gaske yashiga tattaba jikinsa bay yawo da lighter for days like this, yawuce motan yashiga chage motan neman light babu kawao saiya shiga dukan sitarin motan sosai fa kaman da sitarin yake fada, saiya kifa kansa akan sitayin yay shiruuu, tun shigowansa Ammi tagani da Ya Sadiya harda Ibrahim ma, Excellency yayi meeting da kowa na gidan, duk sunsan Habeeb will not agree to this marriage anyi meeting na all of them will work together in uniting them, sunsan ko bayan an kawo Ahlan bazai yarda yayi moving flat dinta ba Ammi plan on that da sauransu da komi agidan nan zasu zauna already abunka da masu kudi yan furniture companies da interior designer na aiki a flat nasu kafin akawo Amarya, dan dago kansa yayi ahankali sai kawai ya kunna motan yaja

wayansa ne yashiga ringing yakalla Ammi ce taka brake yayi saiyakai wayan kunnensa Ammi tace “har yanzu baka iso ba”? Rage muryansa yayi ahankali yace “gani nan zuwa” komar da motan yayi yay parking sai yadan sauke ijiyan zuciya kafin yabude motan yafito yana gyara fuskasa yashiga tafiya ahankali yawuce yabude kofan yashiga falon dake kamshin turaren wuta.
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 30
Kuka Ahlan tayi kukan dabata tabayin kalansa ba arayuwanta, rashin Ummy, tausayin Dr Ashraf, dakuma auren dabatasan wa zata aure ba, auren bazata, auren da ba’a nemi shawaranta ba balle opinion nata, Adda da Ramla sun tsaneta Allah kadai yasan meza’a mata yanzu akai auren nan, yaya Ramla zataji? Tai kuka, jin zata mutu saita tashi tashiga bayi wajajen 3 nadare, tai alwala tafito tai salla, shima kuka tayi all through tana rokon Allah yakawoma rayuwanta mafita, sannan ya tsaremata Ummy aduk inda take, yadawo da ita lafiya.

Idanunta sun kumbura sunyi luhu luhu Mama Mairo tashigo dakin ganin idanun Ahlan saida ta tsorata tace “meya sameki kikai kuka?” Kawai sai hawaye tama rasa mezata ce wani tausayi Mama Mairo taji saita jawota jikinta tace “yakuri hakuri haka aure yake, dena kukan kinji ya isa, tashi kiyi wanka zan kawo miki breakfast masu lallen ki zasu zo by 7” gyadama Mama Mairo kai tayi tace “zan iya kiran kawata Husna tazo?” Dasauri Mama Mairo tace “eh kirata abinda mnakeso kenan ai” gyadamata kai tayi saita dauki wayanta dataga ana a charge ta kunna bazamata iya magana ba WhatsApp message tam Husna tace “I need you Husna kizo kinji”
Sharp sharp Husna tamata reply tace “okay Zanzo anjima kadan” Mama tace “zatazo?” Gyadamata kai Ahlan tayi Mama tace “jeki wanka toh” wucewa tayi bayi, wanka tashiga tafito daure da towel kawai jikinta yamata wani kalan sanyi kaman kankara sababbin kaya tagani akan gadon wani lafiyayyen exclusive atampa irin wanda ake saidawa 1m dinnan an dinka free bubu, Safiya ne tai sallama tashigo dakin taganta tsaye tana kallon kayan, Safiya tace “Mama tace kisaka kifito masu lalle sunzo” gyadama Safiya kai tayi kawai tadauki kayan ta tsaya sai Safiya tawuce ta fita ganin Ahlan nada kunya shiryawa tayi tsaf mai kawai tashafa saita sake zama taki fita lallen ma bataso tayi auren ma bataso tayi bude kofan Mama tayi sallama tayi kawai saita tsaya takasa magana Ahlan kawai take kallo batai kwalliya ko wani abu bane amman Allah yama yarinyar wani kalan kyau da ita kanta Mama bazata iya misaltawaba tace “tun kafin amayi gayu kin fara kyau haka masha Allah tubarkalla, taso muje” tashi tayi ahankali sai Mama tasa hannunta tariketa suka fito ganin jikin yarinyar kaman banata ba, jama’a tagani agidan anata girki gamasu lalle aka zaunar da ita akujera mai kyau jama’a na ayiriri sannan aka fara.

Wuraren 9 Safiya tashigo falon inda akema Ahlan lalle tace “ga bakuwa ki nakawo miki Ahlan” dagokai Ahlan tayi takalli Husna da itama kallon mamaki da rashin fahimtan komi take, kaman jira Ahlan take cus duk duniya banda Ummy Husna itace second closest company datake dashi kawai tabudema Husna hannayenta tana kuka masu lalle suka tsaya Husna itama da jikinta kemata wani irin rawa kawai taje da sauri Ahlan ta rungumeta tadaura kanta akan cikin Husna dake tsaya tana kuka masu lalle duk suka tsaya suna kallonsu da jama’a, bayanta Husna ta shafa tace “ya isa Ahlan stop crying bari agama miki lallen” Mama Mairo ne tazo wajen tace “Babban kawan amarya ta iso” cikeda girmamawa Husna tace “ina yini Mama, Mama tace “sannu Barkan ku da zuwa” cikeda hikima Husna tace “akwai abinda za’ayi ne

Mama” Mama tace “a’a zauna da kawarki halan ganinki yanzu yasa kukan yaragu” Husna tai murmushi tazauna, Mama tace “Safiya zo ku kawo musu breakfast” Safiya tawuce, Husna takara kai hannunta tana share mata hawayen tass takalli masu lallin siata kalli Ahlan tace “what is happening Ahlan? I saw the announcement on news last night I’ve been calling you wayanki kashe, wani irin aure? Did you know him?” Girgiza mata kai Ahlan tayi ahankali tawani Kara ba Husna tausayi, Husna tace “there’s something I wanted to tell you kinsan cewa Dr Ashraf is in love with you?” Wasu sababin hawaye ne suka zubo maya hakan yada Husna tace “kin sani” gyadama Husna kai Tayo tace “he told me rannan da aka kwantar da Ammy”
Saikuma Ahlan takara rushewa da kuka bamatasan mezata ce ba Husna tace “stop crying let’s stop talking about him, you are getting married to another person today, Ahlan most yaran manyan mutane irinku daman yawanci auren hadi ake musu, for political power, money etc, we are children purpose namu is mu cikama iyayenmu burinsu idan what it takes for that to happen is this marriage you can do it, bawai kinada wani tsayayyen saurayi bane ko kinada wanda kikeso ba” Dr Ashraf ne yakara zuwa zuciyanta da fuskansa da yanda take murmushi Husna tace “besides Abban ki and Excellency din that’s shi baban wanda zaki aura seems pretty close so I believe you will be fine, it’s okay kinji kawata, it’s okay kidena kuka” takai hannunta tana share hawayen Ahlan dasuka kasa daina zubowa, ahaka aka kawo 𝕄𝕦𝕤𝕒 abinci Husna tazuba ita da kanta tadinga dena tana sama Ahlan abaki, ganin Husna gave her wani inner strength.
**

Bakin ciki yasa tun bayan yaje masallacin asuba yadawo yana daki, bakin ciki yasa gabaki daya yakasa bacci, wani kalan nauyi yakeji azuciyansa na zafi da fushi, how can adult dashi mai free will babansa zai kama ya aurar dashi.
Wuraren 11 Ibrahim yayi knocking yashiga rike da wasu manya manyan designers bag dakin duhu baya ganin ko’ina, hannu yakai ya kunna wutan dakin, yanda yaga idanun Habeeb dake kallonsa saida gabansa yafadi, yashigo yamaida kofan yarufe zai taka kafa yashigo cikin wata bakar murya Habeeb yace “don’t you dare take another step holding those stuff, turn around and leave this room Ibrahim” baki Ibrahim yabude zaiyi magana Habeeb yadaka masa wani tsawa. “Ibrahim get out!” Kai Habeeb yau ya zuciya baiga any chance na iya yin task din Baba ba, kasa mai magana yayi kawai yajuya yafita yamaido kofan yarufe yahada idanu da Ya Sadiya da Jay dadukaci gayu ya girgixa musu kai, Ya Jabir yace “bari naje nama Ammi magana” saiya wuce ya sauka kasa yafita wajen da Ammi take tareda jama’a ga Hajiya Asabe ya tsaya gefen Ammi, yace “Ammi maganan ki kadai zai iya fito da Habeeb” Ammi ta kallesa anatse tace “kuwuce kutafi I will come now bari na sallami mutanen nan” gyadama Ammi kai yayi yace “let’s go Areef” yakama hannun Areef suka wuce, bakinsu Ammi takalla tace “ina zuwa” tajuya tawuce flat din tashiga Ibrahim kadai tasamu a falo yakalleta wucewa tayi anatse sama, kai tsaye tabude kofan dakin Habeeb takai hannu ta kunna wuta Habeeb yabude jajayen idanunsa yadauka Ibrahim ne Ammi tawuce wajen window tabude window dakin ko’ina adakin yayi haske Habeeb ya runtse idanu, zai juya Ammi ta taho wajen tasa hannu ta yaye bargon tace “tashi tashi kai wanka katafi masallaci” cikin yar karaman murya mai rauni yace “Ammi I’m not going, ba inda zani banda business with this marriage ku kyaleni” Ammi tadade tana kallonsa yanda yamaki kallonta cus bazai iya ya kalleta yanuna mata bata isa dashi ba, cikin irin emotional voice dinnan dake taba zuciyan yaro tace “bari naduka na rokeka toh Habeeb hala hakan yasa kaje” kawai taduka zatasa guiwa kasa wani jumping Habeeb yayi daga kan gado kaman. zaki yariketa idanunsa sunyi ja yacd “Ammi, mehaka? What are you doing?” Cikin raunin murya Ammi tace “idan dukawa na rokeka zaisa kaje wajen daurin auren nan zanje, Habeeb” cikin wani kalan murya Habeeb yace “Ammi don’t make things harder for me than it’s”anatse Ammi tace “Habeeb I am doing opposite of hakan ina saukaka

maka fushin Allah ne, kome ke tsakanin ka damahafinka still mahaifinka ne, idan ka kunyatasa Allah zai tambayeka, is okay idan shi yayi hurting dinka sabida shi mahaifinka but for you Al'ameen is not okay to hurt mahaifinka, koyaya zuciyansa yayi rashin dadi sabida kai Allah zai tambayeka, Habeeb mahaifinka yasoma tsufa, haka iyaye keda rigima suka soma tsufa, as long as ba abinda zai cutar dakai yakeba kamai biyaya yarabu da duniya lafiya"hannunta Ammi takai saman fuskan Habeeb ta shafa tace "the entire manyan mutanen Nigeria today will be at that mosque hatta president na this Country kome babanka yamaka baikamata kasakasa jin kunyan ba'a ga dansa awajen daurin aurensa ba, sabida ni kaje wajen nan Habeeb dina karkaje sabida mahaifinka, kaji do it for me, do it for Umman ka datace nine mahaifiyarku tabani amanan ku, do it for the two of us Habeeb" Ammi ta tsaresa da idanu Habeeb yayi shiru yana kallonta yakasa magana, hawaye ne yaciko idanun Ammi Habeeb na kallonta, bayan hannunta tasa ta share anatse tace "basai Kate ba Habeeb akanme zan dinga saka yin abinda bakason yi saikace Ummank……" "Ammi!" Habeeb yakirata muryansa yay rauni sosai, ahankali yace "don't ever doubt your position azuciyana" Ammi tace "naji bazan karaba, toh idan har inada wannan position na mahaifiyar taka tashi kai wanka ka shirya katafi wajen daurin auren ka Alameen" lumshe idanu yayi yabude su asanyaye yace "toh!" Yabude idanunsa tareda fuzar da iska Ammi saita manna mai kiss a goshi murya cha kasa tace "Allah yamaka albarka son, Allah ya albarkaci auren nan, tashi kaje zansa Ibrahim yakawo maka kayan" ahankali yatashi yawuce bayi Ammi tabisa da kallo yarufo kofa.

🌿 Refresh Your Day with Hamy Green Tea 🌿

Taste the blend that does more than quench thirst.
Hamy Green Tea = Premium Green Tea Leaves + Fresh Mint + Natural Spices

Benefits in every cup:
- Boosts energy & focus, no crash
- Soothes digestion with mint + spices
- Antioxidant-rich for that natural glow
- Clean, aromatic, and made in good condition

Proudly produced by:
Lukuku General Enterprises Ltd
Unit 1 Block D, M.O.W & Trans Technology Incubation Centre, Bauchi

Order/Distributorship: http://wa.me/08095660030
Follow us: IG @lukuku_enterprise | TikTok Lukuku General Enterprises Ltd

Sip healthy. Live fresh. Choose Hamy. ☕🌿
🌿AUREN HADI🌿

✍M SHAKUR

EPISODE 31

🌿 Refresh Your Day with Hamy Green Tea 🌿

Taste the blend that does more than quench thirst.
Hamy Green Tea = Premium Green Tea Leaves + Fresh Mint + Natural Spices

Benefits in every cup:
- Boosts energy & focus, no crash
- Soothes digestion with mint + spices
- Antioxidant-rich for that natural glow
- Clean, aromatic, and made in good condition

Proudly produced by:
Lukuku General Enterprises Ltd
Unit 1 Block D, M.O.W & Trans Technology Incubation Centre, Bauchi

Order/Distributorship: http://wa.me/08095660030
Follow us: IG @lukuku_enterprise | TikTok Lukuku General Enterprises Ltd

Sip healthy. Live fresh. Choose Hamy. ☕

Ammi tai murmushi tajuya tafita daga dakin tana jawo kofa tarufe masa takalli Ibrahim tace “Ibrahim kai masa kayan sawansa” Ibrahim yatashi yace “Ammi karya karamin ihu gashi ki kaimasa da kanki i will wait for him yafito i will drive him to the venue” Ammi ta girgiza kai taja kunnen Ibrahim tace “rago kawai” ta karba kayayakin tajuya tasan yana wanka yanzu saita bude kofan kai tsaye tashiga tanajin karan ruwa tafito da duka kayan ta ijiye kan gado tawuce ta fita.

Fitowa Habeeb yayi daga bayi daure da farin towel a waist dinshi yana kamshi na masifa kaman yasa turare nan ko sabulun wanka ne masu tsada, jikinsa a mummurde gashi da fadi, bakin fatansa nawani kalan sheki, ya kalli kayan dake kan gado yayi jim saiya wuce ya shafa mai yakalli kayan wata mahaukaciyar farin lace din maza ne wanda na kasan sai wane da wane ya isa yasaka irinsa, yadauka yashiga sawa ahankali, Ya Rabbil Alameeen, Lahaulawala quwata illabillahi! Wani irin kyau Habeeb yayi kaman shiyay kansa, yakalli baban rigan sai kawai yadauka yasaka yanajin wani kalan sanyi a jikinsa yarasa dalili yaji wani rahama yashigesa yadauki Rolex agogo yadaura a writs, yadauki farin hulan yasa da takalmi na roberto cover ya Allahu, zama yayi kan gado zuciyansa namai wani kalan sanyi sai kuma bacin rai, jikinsa yamai wani irin sanyi, bude kofa Ammi tayi tashigo tace “Masha Allah Alameen Allahumma Barik tashi tashi” tai maganan tana kwaso turarukansa tashiga fesa masa, sai kawai takama hannunsa tace “muje, muje” Ibrahim yana zaune suka fito he couldn’t believe his eyes ganin Habeeb yafito ango fess ka kallesa saika kara yanda yayi kyau Ango sak, Ammi tace “muje let’s take pictures kafin kutafi” kaman zaiyi kuka ahankali yace “Ammi no pictures please, I hate pictures” Ammi tace “kul, for today kayakuri ayi, today is a special day, muje muje” Ammi tajasa fita waje sukayi wajen backdrop na wedding din da akayi da ballon’s and flowers tace “Hajiya Asabe zoki hoto da danki” sabida da mutane ta taho Habeeb yahade fuska yadauke kai, tazo ta tsaya gefensa, Ammi ta tsaya dayan gefen camera man yadauki hoto, Ya Sadiya tazo kowa akai hotuna ko murmusi daya bayayi Ammi tace “kutafi toh yanzu karkuyi latti” har mota takai Habeeb yaashiga Ibrahim yaja Motan da gudu suka sharara around 1:30 sukakai central mosque.

Kunga jama’a kunga mutane, suma sabida ango ne a motan nan da nan aka gyara musu security suka shiga, there’s something da Habeeb yakeji ajikinsa da he can’t even explain, sai kallon jama’a yake yanzu wai duk sabida shi aka cika wajen nan, Ya Jay ne yataho yana gyara babban rigansa tareda Areef shiya bude bangaren Habeeb suka hada idanu da Habeeb, wani murmushi YaJay yamasa yace “Allahumma Barik let’s go” Areef yace “Uncle Habeeb kayi kyau” ahankali Habeeb kaman bazaiyi magana ba yace “can you give me your glasses?” Dasauri Ya Jay yazare black shade na rayban dake idanunsa yaba Habeeb karba Habeeb yayi yasaka wani dadi Ya Jay

yaji yafito anatse yana sauke kafansa, Ya Rabbi wani chills yaji ajikinsa he don't accept this marraige why is he feeling somehow kaman irin rannan means something to him dinnan, Ya Jay yace "muje" shine agaba Habeeb da Ibrahim suka jero some bodyguards na Abba na biyedasu saiga mawaka masu busa kalangu sun zo. "Takawanka lafiya Ango mai capacity, Barrister Alameen Habeeb jarumin samarin bana, zakaran gwajin dafin Excellency, son kowa kin wanda yarasa, yaro mai kama da babansa" a kofan masallaci yahada idanu da Excellebcy dake cikin shiga ta alfarma, daura idanunsa dayayi kan Habeeb wani ijiyan zuciya ya sauke fara'an fuskansa yakara watada, Abba dake tsaye tareda shi shima ya tsare Habeeb da idanu yadade baiga Habeeb ba morethan 8yrs, ganinsa yau saiyaga he's not that Habeeb of 8yrs back, wannan Habeeb din lafiyayyen tsayayyen namiji ne anan mai hankali da natsuwa dakuma kamala that's all he sees, Habeeb na isowa wajen Abba ne yabasa hug yace "Assalamu alaykum son" sauke kansa kasa Habeeb yayi yakasa magana yakasa cewa komi, yau saiyaji yanajin nauyin Abba, Abba yasake sa ahankali, Excellency yakamasa yace "mu shiga adaura" shiga sukayi aka zaunar da Habeeb ahankali Excellency yazauna kusa da Habeeb masu camera da video sai hoto suke dauka, Governors, ministers, suwaye da waye are all around liman yafara gyaran speaker sai yafara magana. "Innal hamdalillah, Nahmaduhu wanasta'inuhu wanastagfir……" tass liman yagama jawabinsa yace "waliyin amarya da waliyin ango suna nan…" kirjin Habeeb yashiga bugawa dum dum dum! Aure ba abin wasa bane, fadansa, matsala sa da mahaifinsa is one thing, aure is another thing, responbility wata hakki dasauransu na kansa, daidai yadawo daga tunanin yaji liman na cewa. "Jama'a ku shiga wannan daurin aure tsakanin Alameen Habeeb, da Ahlan Noor akan sadaki naira Miliyan goma da tasan gwal dari" yan masallaci akai kabbara zuciyan Habeeb kaman zai fita, shikenan? He's a married man? Innalillahi wa innailaihi raji'un! Liman yace "yakai Ango kasani cewa an rataya muku igiyoyi guda uku na aure, daga lokaci irin ta yanzu hakkoki na Ahlan yadawo kanka, wajibi ne agareka ka ci da ita, ka shayar da ita, ka tufatar da ita, kabata muhalli makwanci mai kyau, ka tsareta daga cutarwa, ka killaceta, ka kare hakkokanta ka zama wanda zai nuna mata hanyar kwarai hanyar koyarwan annabinmu Muhammad SAW, muna addua Allah ya sanya albarka a auren nan, Sallu ala nabiyil Kareem" SAW akai salatin Annabi aka shafa aka tashi, nan fa aka fara gaishe gaishe Ibrahim ya kallesa yanda yama kasa motsi yace "tashi muje Ango" wani kallon Ibrahim yayi dayay maza yace "yakuri maida wukan wasa nake, ang oh I mean Habeeb, let's go" tashi Habeeb yayi ahankali kawai sai Excellency yadafa akafada yana murmushi yana kallon camera man yace "snap me and my son together" hade fuska Habeeb yayi ba yanda zaiyi duk jama'a hoto aka musu Excellency yasakasa yayi hotuna da manyan mutane da Abba duk zuciyansa ba dadi sai da akai la'asar a mosque dinnan suka fito, bodyguards biye dasu, ahankali suke tafiya shida Habeeb da Ya Jay da Areef har lokacin da jama'a sosai, zasu wajen dasukai parking kaman daga sama aka wani kalan bangaje Habeeb irin mugun bangajewan nan saida Habeeb yay baya dasauri ya tsaya da kyau chak like a man that he is, kowa na wajen yajuyo harda bodyguards din dan bangajewan doesn't look like na mistake, cikeda bacin rai Ya Jay yace "Malam baka ganine" bodyguard sukai kanshi Ya Jay yace "kubarsa" cus akwai jama'a, Dr Ashraf ya tsaya chak yana kallon idanun Habeeb dake cikin dark shade shima Habeeb kallonsa yake from glasses din, kallon Habeeb Dr Ashraf yake kaman zai kashesa, har yanzu robe din jiya ne a jikinsa ne na hospital, yunkuri yayi zai tako yazo dab da Habeeb bodyguard suka taresa. "Malam lafi….." "is he here for you gentleman or did I assign any of you for protection?" Bodyguards din suka juyo suka kalli Habeeb, da hannu yamusu alamu yace "let the youngman through" suka matsama Dr Ashraf kaman jira yake yataho gaban Habeeb ya tsaya dab da shi yana wani irin huci, cikin murya na tsantsan kishi yace "if you are waiting for sorry dan na bugeka that's not gonna happen you hear me" sosai Habeeb ke kallonsa baice masa kala ba, cikin wata kalan murya mai bala'in zafi sabida Habeeb bai kulasa ba Dr Ashraf yace "I have something to say to you dan kaji, better treat Ahlan well, karkai kuskuren hurting nata, kar……."

Habeeb dakeji da zafin zuciya cikin kakkausan murya yace “idan anyi fa?” Dasauri Ya Jay yashiga gaban Habeeb cus he knows waye Habeeb ya zamto shine ke facing Dr Ashraf yace “Malam I don’t know you, I’m sure my brother doesn’t know you, we don’t want trouble, idan wat you said just now shawara ce to the new ango zai dauka mun gode let’s go Habeeb, start the car Ibrahim”Ibrahim yawuce Ya Jay yajuya yaja Habeeb yace “let’s go!” Habeeb kaman bashi aka ja ba ko gezau baiyiba wani kallo yakema Dr Ashraf dashima yaki moving kallon Habeeb yake yana wani kalan huci yana dunkule hannu……
AUREN HADI

✍M SHAKUR

EPISODE 32

*Refresh Your Day with Hamy Green Tea *

Taste the blend that does more than quench thirst.
Hamy Green Tea = Premium Green Tea Leaves + Fresh Mint + Natural Spices

Benefits in every cup:
- Boosts energy & focus, no crash
- Soothes digestion with mint + spices
- Antioxidant-rich for that natural glow
- Clean, aromatic, and made in good condition

Proudly produced by:
Lukuku General Enterprises Ltd
Unit 1 Block D, M.O.W & Trans Technology Incubation Centre, Bauchi

Order/Distributorship: http://wa.me/08095660030
Follow us: IG @lukuku_enterprise | TikTok Lukuku General Enterprises Ltd

Sip healthy. Live fresh. Choose Hamy. ☕
Mamanta bata iya yinsu ba, ya rokemu kan mukoya mata girki which Inaso kabarta ta dinga zuwa side na Ammi tana koya dakuma wajen Asiya matar Ibrahim kaga kusan kansu daya Asiya zata iya bata shekaru kadan but she will learn freeely dasu, idan kuma zaka dauko mai koya mata ne duk daya, Alameen listen fadanka da babanka I understand you saisa kaga bantaba shiga ba, amman idan har kabari fadan ya shafi this innocent girl koka cutar da ita seriously Alameen zanyi fushi dakai mai karfi, zan dinga zuwa time to time ina dubaku, Safiya zata dinga zuwa, take care of matarka kanajina" gyadama Mama Mairo kai yay ahankali tamike tsaye tace "bara naje za'a kawo muku breakfast aka gama"tamike tawuce Habeeb na zaune awajen kaman maganan yatabasa yakai kusan 5min sanna yamike ahankali yabude kofa yashiga flat dinsu, maida kofan yayi yana kallon ko'ina ta kwashe komi nata saiya wuce sama yana tafiyan nan daidai hannu yasa zai bude dakinsa sai ya tsaya ya kalli dakinta yana tuna maganan Mama Mairo saiya tsaya gaban dakinta hannu yasa ahankali yay knocking fitgita Ahlan dake kan gado tayi jin knocking ahankali tace "yes" ta tashi zaune akan gado tana kallon kofan gabanta na faduwa, jin shiru saita sauko daga gadon ahankali closet tashiga tadauko hijabin datake salla dashi tasaka tazo wajen kofan ahankali yabude kofan ganin Habeeb tayi kaman wani zaki tsaye gaban dakin dasauri takoma baya tasauke kanta kasa tashiga wasa da fingers nata, dakin Habeeb yabi da kallo dake kamshin turarukan datai using bayan tai wanka kafin yadawo da idanunsa kanta navy blue hijabin yamata kyau dasauri yadauke kansa yace "is something wrong with your mouth"? Kirjinta na dukan uku uku Ahlan ta girgizamai kai hawaye na zubowa daga idanunta cikinta na kugi sabida yunwa dasauri tadaura hannunta daya saman cikinta ta saman hijabi Habeeb yadawo da idanunsa kanta, kanta akasa cikin voice da tone na kuka tace "good morning" kaman bazaiyi magana ba da kyar yace "did somebody beat you?" Girgizamai kai Ahlan tayi dasauri, strictly yace "kukan na menene"? Hadiye kukan tayi takai bayan hannunta tana goge fuskanta dayan hannun tanadan matsa cikinta dake bitting nata sabida yunwa this days batacin abinci mai kyau da yawa, Habeeb adanyi shiru yarasa mezai ma ce shi baimasan tayaya zai kula da itaba yajuya cikeda takaici, saikuma ya tsaya yajuyo she's still cleaning tears da hannu daya dayan hannun na saman cikinta tanadan kama cikin ta saman hijab batamasan tanayi ba, ahankali Habeeb yace "are you hungry?" Gyadamai kai Ahlan tayi da sauri, cikin fushi yace "baki da baki?" Kuka na neman kufce mata tace "yun….yunw…. Yunwa nak…."kawai juyawa Habeeb yayi bai tsaya jira ta karasa ba she looks very hungry yasauka kasa zama yayi kan kujera yaciro wayansa number Ya Sadiya yayi dialing ringing daya ta daga tace "Ang…." Kafin tai magana yace "is breakfast not ready Yaya?" Ya Sadiya tace "eh but akwai tea and bread da chips" dan jimmm yayi yanajin kunya cus zatasan bashi bane, bayashan tea sai coffee, yadake yanacin magani yace "please send it" Ya Sadiya tace "okay bari nasa Safiya takawo, wazaici kaine ko Ahlan?" Sauke wayan yayi daga kunnensa ya katse batare daya amsa ba, yadaura kafa daya kan daya, kusan 5min yana zaune awajen aka danna doorbell, mikewa yayi yawuce wajen kofa yabude, Safiya ce tsaye tana ganinsa ta washe baki tace "Ya Habeeb ina kwana" tai maganan zata shigo cikin falon hannu yabata alamun tabasa baya bukatanta ciki, ko kadan bataso ba, taso taga Ahlan amarya, basa tayi ahankali amman takasa daurewa tace "Ya Habeeb ina Ahlan?" Wani kallo yamata yace "kin bani ajiyanta ne"? Akunyace Safiya tai murmushi, zatai magana ya maida kofan yarufe yajuya hanyar dinning yayi ya ijiye tray din kan dinning table, sai yawuce kitchen bottle water yadauka mara sanyi yafito yadauki tray din yawuce sama har zuwa gaban dakin hannu yasa yay knocking, Ahlan na kwance kaman marainiya taji anyi knocking again, mikewa tayi ahankali zata dauki hijab data cire yana kam gado tasaka kai tsaye Habeeb yabude kofan dasauri ta kallo kofan har lokacin da ruwa a idanunta taji tsoro ganin yabude kofan da kansa, tsayawa yayi wajen kofa yakalleta baiyi magana ba, dasauri Ahlan tasaka hijab din tazo wajen saita kasa karasowa gabansa ta karbi tray din sabida tsoro ta tsaya nesa dashi ta sauke kanta kasa, shigowa dakin yai anatse wani sanyi Ahlan taji na bin jikinta jin yashigo dakin ya wuceta kaman bai ganta ba ya ijiye tray

akan gado da ruwan yajuya yafita daga dakin yarufo mata kofa batare daya cemata kala ba, Ahlan tabi kofan da kallo saita koma ahankali wajen abincin tabude tray da wani clean towel na rufe abinci da aka rufe taga chips egg da bread sai tea wlh she’s so hungry ahankali tashiga ci tana sauke ijiyan zuciya.
EPISODE 38

Abincin yamata dadi sosai sama dana gidansu da Hajiya ke dafawa, ahankali takeci saita mike tsaye tasauko daga gadon tawuce tadauko babban jakan makaranta ta taciro laptop tadawo tabude laptop din, hoton skeleton ne a background din sai ita da Ummy a tsakiya, shiru tayi tana kallon Ummy saita bude file inda films dinta ke ciki, tasaka wani anime, rabon da tai kallo ta manta, kawai batason bakin ciki ya kasheta ne, cartoon din take kallo tanacin chips din da egg kusan 1hr tayi tanacin abincin tagama bataci bread ba but ta cinye chips din da egg da tea, sauka tayi dagakan gadon tadauki hijab tasaka, slippers dake dakin pink tazura kafanta ciki saita bude kofan dakin ahankali kaman barauniya tafito, bata rufe dakin ba cartoon nata yacigaba da aiki dan batai pausing ba tawuce tashiga sauka kasa.
Ahankali Ahlan tasa hannu tabude kitchen din, kitchen din yayi kyau sosai sai kallo take, wajen sink tawuce ta wanke komi tafito daidai ana danna door bell tasan ba shi bane hakan yasa tafito kaman mara gaskiya saita wuce wajen kofan tasa hannu tabude, Safiya tagani tareda Ya Sadiya, Safiya ta washe baki tace “Amarya kin tashi lafiya” akunyace Ahlan tamika hannu cikeda girmamawa zata karbi kayan hannun Ya Sadiya tace “ina kwana Anty”cikeda fara’a Ya Sadiya tace “no Amarya bata aiki bari naje na ijiye dakaina, shiga kiga Safiya” cikeda kunya kaman zatasa hijab a bakinta Ahlan tace “dan Allah ki kawo” Ya Sadiya tabata tace “tom gashi godiya nake” karba Ahlan tayi tajuyo karaf tahada idanu da Habeeb dake bene yana saukowa kwata kwata bakajin step nasa, ya kirne fuska sosai kaman bai taba dariya ba, yana sanye cikin suit baki yay bala’in kyau, dasauri ta ijiye kanta kasa tawuce dinning Ya Sadiya tace “sai ina?” Yana kallon writs nasa yace “office I have meeting” Ya Sadiya tace “to kayi breakfast before going out” anatse yace “azumi nake yau” idanu Ya Sadiya tazaro tace “yau sunday fa azumin me kake”? Baice mata komiba kawai yawuce yabude kofa yafita, Ya Sadiya tarike dariyanta kar Ahlan ko Safiya su gane wani abu, ta taho dinning din tace “Safiya maza je dauko sauran abubuwan” Safiya ta mike tace “ina zuwa Ahlan” Ahlan ta gyadamata kai tawuce tafita, Ya Sadiya tazauna kusa da Ahlan da kanta ke kasa tana wasa da yatsunta tace “kin sanni?” Girgixa mata kai Ahlan tayi, Ya Sadiya tace “sunana Halimatu Sadiya nine yayan mijinki Habeeb, daga Yaya Jibril damuke kira Jay, sai ni, sai Habeeb, mu uku Umma ta haifa, ina gidan nan for now sai next week Friday zan koma idan mijina yadawo daga Russia, if you have any problem ko Habeeb yamiki wani abun you can report him to me kinji, ki daukeni a matsayin babban yayanki” gyadamata kai Ahlan tayi ahankali, Ya Sadiya tabude farfesun mata da tsumi da aka hada mata tace “nasan kinyi breakfast but try kici wannan maganine is good for your health and body” gyadamata ka Ahlan tayi tace to, Ya Sadiya tadauki spoon da kanta tabata ahankali Ahlan ta karba tace “nagode” itadai Ya Sadiya tanason yarinyar wallahi, tanada natsuwa, she’s so innocent and pretty, gatada shiga rai, kuma batada rashin kunya ko tsiwa, murya chan kasa cikeda so Ya Sadiya tace “Ya Habeeb yamiki fada ko wani abu”? Dasauri Ahlan ta girgiza kanta tace “a’a” Ya Sadiya tace “I’m serious idan koda wasa yamiki wani abu dabakiso zaki iya kawo karansa wajena ko wajen Ammi kinji” gyadamata kai Ahlan tayi tadauki tsummi tasha tandan bata fuska Ya Sadiya tai dariya tace “likita da batason magani” daidai lokacin Safiya na dawowa da kaya niki niki tazo ta ijiye, doorbell aka danna Safiya tamike dagudu taje tabude kofan tace “laaaa Anty Asiya” daga Ya Sadiya har Ahlan suka juyo suka kalleta tana sanye da atampa Riga da skirt mai kyau da mayafi cikinta yadan fito kadan dudda is just 4months old, Ya Sadiya

tamike tace “zonan ki zauna” Asiya ta taho tana murmushi tace “tuntuni nake jira naga Ya Habeeb yafita nazo, nidai kaf gidan nan tsoro Ya Habeeb kebani Ya Sadiya” aka kwashe da dariya banda Ahlan dake jinsu, Ya Sadiya tace “Habeeb nada kirki fa kuma ka zauna dashi saikaga ba mafadaci bane at all daga waje ne zaka dauka madafaci ne but he’s very gentle especially with girls, tunda kinzo bari na barku, Safiya muje akwai inda zaki rakani” Safiya ta mike tanadan turo baki dan tafiso tazauna dasu Ahlan, Ya Sadiya tajata tace “muje anjima kya dawo” wucewa sukayi suka fita Ahlan tadan sauke kanta kasa tace “ki zauna” Asiya ta taho ta zauna kan kujeran dake kusada Ahlan ahankali takalli Ahlan tace “can we be friends Ahlan? I’ve been so lonely Allah yasani da akace za’ama Ya Habeeb aure I was so happy atleast xan sami sister kullum ina daki, Ammi kuma kunyanta nakeji bana iya hira da ita sosai, da Ya Sadiya tazo ne ma naji dama dama, kinga yanzu kinzo zan dinga zuwa wajenki hira kema kina zuwa wajena ko”? Gyadamata kai Ahlan tayi ahankali, batasan mezata ce ba but kuma taji dadin ganin dukansu sai damuwan yaragu sosai atleast duk sunada kirki, shiru sukayi, chan Asiya tace “Auren Hadi nada dadi don’t be too sad about it Ahlan trust me” dan kallonta Ahlan tayi saita sauke kanta kasa ahankali, Asiya tace “da gaske ni wlh ina sonki we are dsame age group but nabaki 2yrs I’m 22, so I mean no harm, and hiranmu remains tsakaninmu bazan tab fadama Ya Habeeb ba nasan abinda kike tsoro kenan, kinsan mesa nace Auren Hadi da dadi?” Dago kanta Ahlan tayi takalleta saita girgiza mata kai, Asiya tace “kin taba soyayya da wani Ahlan?” Girgiza mata kai Ahlan tayi alamun a’a, Asiya tadanyi murmusi tace “kinga akwai Yayata sunata Ya Amina, Abban mu yahada ta aure dawani Yaynmu, ba Abban mu ya haifesa ba dan yayan Abban mu ne yarasu so agidanmu yataso kawai kwatsam rana daya Abba yace zai hadasu aure basason juna, akai biki kinsan agidan suka fara soyaya, yana sonta fiye da komi, itama tana balain sonshi, tunda baki taba son wani ba nan da nan zakiso Ya Habeeb shima” dadan sauri cikeda zuciya daya Ahlan tace “Dr Ashraf!”

EPISODE 39

Asiya dake kallonta tace “waye Dr Ashraf”? Sauke kanta kasa tayi baki tabude zatai magana saiga kuka dasauri tasa hannu ta goge da bayan hannunta, asanyaye tace “I feel so bad for him, I feel kaman na yaudare shi, kaman I am a bad person” Asiya takai hannunta ta taba cinyanta tace “Ahlan you are not a bad person kidena cewa haka” cikin kuka wanda daga zuciyanta yake tace “yanada bala’in kirki, yace baisan fuskana ba yafara sona 4yrs ago ranna da aka fara kamu asibiti, he helped me look for Ummy na saida yaji ciwo because of that, rannan yace yana sona nabasa permission yaje yaga Abba nace no, yace inada wanda zan aura ne I told him no, just for him maybe to see announcement din a TV, he’s too good to be hurt like that” tarushe da kuka Asiya tai shiru tana kallon Ahlan cus in all maganan da Ahlan tayi bataga wani sign na eh Ahlan loves Dr Ashraf dinba, wat she sees is zuciyan Ahlan recognizes mutumin as mutum mai kirki yatayata neman Mamanta she’s grateful, sannan shine wanda yafara cewa yana sonta da sauransu, but zuciyanta yafi rinjaya a tausayin mutumin takeji, ahankali takai hannunta kan fuskan Ahlan ta share, murya chan kasa tace “haka Allah yayi ke ba matarsa bace, stop talking about him ki manta dashi, kin zama matan wani koda bakison auren nan dole ne ki kare mutuncin auren kinji, karki kara maganan sa, sannan karki kara magana dashi” gyadamata kai Ahlan tayi tana sauke Ijiyan zuciya tace “I feel so bad, I don’t want to see him, idan gobe monday naje hospital zanje a chanzamin Unit wajen HOD dinmu cus a unit nasa nake, that’s the right thing to do ko Ya Asiya?” Dasauri Asiya tace gyadamata kai tace “yes is the right thing to do Ahlan, yana sonki gwara ki nisanta kanki dashi is for your own good and his own good”Asiya ta kalli magungunan tace “shanye tsumin nan is very good” shanye wa Ahlan tayi, Asiya tace “bari naje na gaida Ammi banje flat dinba

yau gabaki daya” ahankali Ahlan tace “zan biki” dasauri Asiya tace “a’a zauna anan bakisan Amarya bata fitaba” kaman zatai kuka tace “dan Allah zan biki, ni ba Amarya bace” dan jim tayi tace “ina zuwa” wayanta Asiya tadaga tai dialing number Ammi, ringing daya Ammi tadaga tace “daughter na lafiya dai ko hope nothing is wrong”? Murmushi Asiya tai tace “lafiyana kalau Ammi daman ina side din Ahlan ne nace mata zanzo na gaidaki wai zata bini nataho da ita Ammi?” Ahankali Ammi tace “eh kuzo tare dole ta gaji ita kadai a barayin nan” Asiya takalli Ahlan tace “jeki chanza hijab ki sa kaya mai kyau da mayafi saikizo muje” Ahlan ta gyadamatakai tajuya dasauri tawuce sama Asiya na binta da ido kana ganin yanda takeyi kasan zaman nan ya isheta, saitasa hannu tadauki kazan data rage takai kitchen tai packing nasa tasaka a fridge anjima zata iya microwaving tafito jikinta ciwo yake, Ibrahim akwai fitina tunda tai cikin nan saiya karu the only time take hutawa is idan bayanan, saukowa Ahlan tashiga yi Asiya tadaga kai ta kalleta tana sanye da pink lace riga da skirt ya kama jikinta daidai shape na curvy ass nata yafito da cikakken kirjinta tana kamshi yarinyar akwai kyau ga gyale da dan kwalinta a hannu ta taho tazo wajen Asiya dan kwalin tabata tacd “dauramin” karba Asiya tayi tana shafa gashin Ahlan tace “Ahlan bantaba ganin dogon gashi hakaba” ahankali Ahlan tace “ni banaso bana iya gyarawa, Ummy ke tayani, tunda ta tafi ban kataba sai jiya” takarasa maganan ahankali feeling sad Asiya tace “zauna na daura miki” zama tayi Asiya ta daura mata dan kwalin simple style tadanja dan kwalin baya ana ganin gashinta ta gaba ta yafa mata gyalen aka tace “muje” mikewa Ahlan tayi suka fito tare, kawai tagaji da flat dinne tabi compound din da kallo daya hadu sosai da suka wuce flat na Ammi dakeda dan tafiya Asiya tabude kofan da sallama Ammi na zaune a falo tana magana da wata mai tayata aiki Ahlan ta shigo kanta akasa dakin kamshi, Ammi ta kallesu Asiya ta taho wajen Ammi dasauri tace “Ammi ina kwana” Ammi tace “lafiya lau kin iya kinci abinci yau hope baki amai ba” adan kunyace tace “banyi amai ba Ammi” Ammi ta kalli Ahlan data tsaya daga baya kanta akasa tace “Ahlan taho nan” takalli yar aikin tace “you can go Talatu” ahankali Ahlan ta taho har gaban Ammi zata duka Ammi tace “no no” akunyace tace “ina kwana Ammi” murmushi Ammi tayi tace “mun tashi lafiya ya kwanan sabon wuri da kewan gida, sit here” tazaunar da Ahlan gefenta Asiya ta zauna kan one sitter tana murmusi tace “Ammi ina su Ya Sadiya”? Ammi tace “sun fita itada Safiya just now” Asiya ta gyadakai Ammi tasake kallon Ahlan that is not comfortable tasa hannunta takama habanta tace “be free kina dakin Mamanki ne nan kinji, this is your house” gyadamata kai tayi ahankali cikeda kunya, Ammi tadubi Asiya tace “Asiya tashi kaita kuje ku gaida Hajiya Asabe” tashi Asiya tayi tace “let’s go Ahlan” ahankali Ahlan ta mike tabi bayan Asiya suka fita Ammi tabita da kallo tadan sauke ijiyan zuciya, anjima da rana mai gyara zata iso cus tasan babu gyaran da akama yarinyar, flat din Hajiya Asabe Asiya tai sallama ta shiga tana zaune a falo da plate a hannunta tanashan fruits kallo daya tama Asiya ta watsar ta bi Ahlan dake bayanta da kallo, Asiya ta maida kofan tarufe takama hannun Ahlan sukazo gaban Hajiya Asabe suka duka ahankali tace “ina kwana Big Mommy” Ahlan tace “ina kwana big Mommy” tabe baki tai tace “lafiya, wannan kuma fa” tanuna Ahlan da baki, Asiya tace “Matar Habeeb ce Ahlan” Hajiya Asabe tace “Kice matar gogan dayafi karfin gidan, ke kalleni nan” ahankali Ahlan tadago kanta ta kalli Hajiya Asabe faduwa gabanta yayi Hajiya Asabe tace “su Ramla fa”? Bugawa kirjinta yayi bakinta na rawa rawa tace “lafi…lafiya lau” Hajiya Asabe tace “yakamata Ramla tazomin hutu” mikewa Asiya tayi tace “bari muje” tadago Ahlan, Haiiya Asabe tama Ahlan wani mugun kallo tace “to nagode da gaisauwa”

Suka wuce suka fita flat na Ammi suka koma suka shiga Ammi tace “Ahlan tashi kuje kitchen ku taya talatu girki” tashi Ahlan da Asiya sukayi, zasu wuce Ammi tace “kawo mayafin nan” zare mayafin Ahlan tayi taba Ammi ta karba suka wuce kitchen, girki suka fara, Talatu na musu hira, for the first time saitaji abu yadauke mata hankali, she really can’t do much a kitchen daga Asiya har Talatu saida suka lura sai suka dinga nuna mata step by step na komi tana kallo and she was so happy to learn ita ke sa maggi tajuya more like ita kesa komi ana bata instruction she was really very

happy, Ammi taleko kitchen din, ajiyan zuciya tasauke ganin Ahlan tasaki jiki sosai tana girki she was smiling abinda bata taba ganin yarinyar tayi ba, she really like Asiya, burinta ya cika matan yaranta su hada kai, ajiyan zuciya tasauke, juyawa tayi takoma babu wanda ya lura ma da ita.

Around 4:15 yashigo gidan tareda Ibrahim, parking motarsa yayi suka fito tare suka shiga tafiya direct flat din Ammi sukayi, Ibrahim yafara bude kofa yana biyeda shi abaya suka shiga Ammi ne a falon da Ya Sadiya dakuma Ya Jay, sai kannin Mijin Ya Sadiya Mubarak dayazo duba Ya Sadiya, daidai Ahlan na fitowa daga kitchen tareda Asiya kowaccen su na rike da warmer, Ahlan na magana da yar karaman muryanta tace “Ya Asiya abincina yayi dadi ko”? Karaf maganan yasauka a kunnensa, dago kansa yayi ya kallo wajen Ahlan akan idanun kowa na dakin dake kallonsa banda Mubarak daya kalli Ahlan din dan this is the first time dasuke fitowa daga kitchen tunda yazo, tana tafiya rikeda food warmer tareda Asiya, daga ita sai riga da skirt na lace dankwalinta yaja baya sosai ana ganin almost rabin gashinta, rigan yakamata like you could see sama saman boobs nata dasuka taso, hakanan wani abu kawai yaji a wuyansa mai balain daci da tauri kaman maruru amman na wuta, Ammi tace “ahhh Alameen kun dawo?”Chak Ahlan ta tsaya jin sunan wanda aka kira, itama Asiya tajuyo tahada idanu da Ibrahim daya kashe mata idanu daya tadauke kai dasauri, ahankali Ahlan tasauke kanta kasa ta ijiye kulan tajuya zata koma kitchen Ammi takalli yaran tace “Ahlan an gama girkin”? Tana tsaye daga wajen jikinta yadan fara kyarma yarinyar da lafiyanta kalau, gyadama Ammi kai tayi takasa magana da kyau tace “uhnn” Ammi tajuya ta kalli Habeeb cus ganinsa yasa yarinyar ta dimauce, Ammi tace “akawo muku nan ko a dinning zakuci Habeeb da Ibrahim”? Mubarak dake kallon Ahlan yace “a dinning zanci Ammi” Habeeb yai kofa, Ammi tace “magana nayi Habeeb” dan tsayawa yayi bai juyoba da kyar yace “azumi Ammi, bari naje na watsa ruwa” muryansa gabaki daya ba dadi, dawani kalan sauri Ahlan takoma kitchen Asiya tabita da kallo itama, Ammi dake kallonsa zai bude kofa tace “azumi kuma Habeeb yau Sunday fa” Ibrahim ya mugun dagewa ya danne dariyan dayakeji mamaki ya kashesa na Habeeb, daga hadasa da mace waje daya shine harya fara azumi, Ya Jay ma haka shi yasan da kyar idan Habeeb bazai zama mabukaci ba, Ammi dai bata gane komiba, Habeeb yarasa mezai cema Ammi ganin tana jiran amsa bai iya karyaba abu yataba faruwa dashi last Ramadan yayi rashin lafiya amman still baisha azumi ba hakan yasa ahankali yace “I was sick last Ramadan” dasauri Ammi tace “ayyooo” ahankali yace “bari nai wanka Ammi” yawuce yafita Ya Sadiya takawo bakinta saitin kunnen Ibrahim tace “Ibro explain to me ana kishin abinda ba’aso ne” Ibro yace “your brother is special case, murdadden mutum fa bahaggon mutum ne” Ammi tace “wai ku kun girma baku dena gulma ba” sukai dariya, Ammi tace “Asiya kira Ahlan tabi mijinta yadawo”.

Flat nasu Habeeb yawuce yabude kofa ko’ina agyare, akwai abinci a dinning, magana yakeji kasa kasa more like yana fitowa daga device hakan yasa yawuce sama kofan dakinta abude ga laptop akan gadonta dake magana yay jimmm ya tsaya kafin ahankali yataka yashiga dakin yakai hannunsa yasa yajuyo da laptop din anime take kallo it’s season automatic yake shiga next episode, hannu yasa yayi clicking on pause sai yajuya yasa hannu ya kashe wutan dakin yarufo kofan ahankali, yakalli staircase kaman yana jiran abu, saiya wuce yashiga dakinsa sai yafito yashiga saukowa yadawo falon yazauna yadaura kafa daya kan daya kusan 20min yana zaune yana kallon kofan yaji ana taba kofan.
EPISODE 40

Ahankali Ahlan tabude kofan kirjinta na dukan uku uku, this time tayafa gyalenta tundaga ka, kanta akasa amman taji kamshin turarensa shigowa tayi ahankali tamaida kofan tarufe saita kasa motsi tarakube jikin kofa, cikin wani irin kakkausan murya mara wasa Habeeb yace “da izinin wa kika fita?” Wlh kirjinta bugawa yayi rasss! Tarasa mezata ce kawai jitayi tajuya da dan saurinta zata bude kofan takoma wajen Ammi Habeeb yamata wani mugun tsawa. “Keh!” Afirgice Ahlan tasaki hannun kofan tafashe dawani mummunan kuka, mikewa tsaye Habeeb yayi ranshi kawai yabaci sosai yashiga tahowa inda take zata duka yace “don’t even try it!” Ya tsaya dan nesa da ita, cikin tsananin zafin murya yace “waya baki izinin fita?” Ahlan na kuka ta manne jikin bango tace “wajen Amm……” “did I tell you to go there?” Yafadi rai abace, Ahlan ta girgiza masa kai takasa kallonsa, Habeeb yace “namiki kama da those men dake sakin matansu to be everywhere?” Sake girgixamai kai tayi, wlh he’s very angry zuciyansa tafarfasa yake yace “free will dinki yakare agidanku since Babanki decided yamiki auren siyasa, you must live by my rules, my regulations, my terms and my conditions, you can’t go anywhere without my permission ko kidinga yawo in anywhere ba abu jikinki wat is the meaning of that bakisan maza na shigowa side dinba?” Yadaka mata tsawa mai kyau yace “you think inason auren nan? This marraige is nothing but a burden arayuwana, azuciyana, ban samu nayi yanda nakeso ba, you think you will get to do yanda kikeso? You are not allowed to step out of this door without permission hence forth am I clear”? Kai Habeeb is another thing idan yayi fushi, gyadamai kai tayi jikinta na tsuma, strictly yace “banson yawo, banson shige shige, banson tarin unnecessary kawaye, banson surutu, for the last time, you are not allowed to leave this room without my permission!”Yajuya cikeda zuciya fuuuu yawuce sama, Ahlan taduka wajen tana kuka sosai, lh this few hours dayake side na Ammi especially sanda take girki ta mance komi harta manta ma anmata wani aure da bataso, but yanzu sai komi yadagule mata tadade awajen tana kuka ta tashi takoma kan kujera ta kwanta ahankali tsoron zuwa sama takeji in all this things dake faruwa Ummy ta kawai take kewa, tana kwance akan kujeran har wajajen magrib taji ana bude kofan sama dasauri ta tashi zaune saukowa yayi ko kallon inda take baiyiba yawuce yafita hakan yasa itama ta tashi dasauri tawuce sama tashiga maida kofa tarufe, tana daki asama taji ana danna doorbell saita sauko tazo tabude kofan Safiya ce tana kallon idanunta tace “kuka kikayi? Ya Habeeb yamiki fadane halan?” Dasauri Ahlan tace “a’a” tasa hannu ta karbi tray din Safiya tabiyota tana kwasan kulolin dazu tace “Ammi tace ki shanye farfesun, kuma saina gayamata kinyi kuka” dasauri Ahlan tace “gashine fa yashiga idanuna” Safiya tai shiru tace “tom shikenan bari naje” tawuce tafita Ahlan takoma sama tashiga cire kaya dantai wanka.

Ana gama sallan magrib yadawo, bude kofa yayi yamaida yarufe yazo wajen tv ya kunna saiyazo dinning yaja kujera ahankali ya zauna yadeba ruwa a jug yasha saya bude warmers din pepper soup cow tail yadeba yashiga ci anatse yanashan juice yana wajen har aka kira isha’i saiya wuce yakara fita yayi salla around 9 yashigo, plate dayaci abincin yadauka yawuce kitchen da kansa ya wanke ya ijiye gefen sink yafito yawuce sama, agaban dakinta ya tsaya yakai hannu yayi knocking Ahlan dahar ta kwanta gabanta yafadi sosai, taki motsi, bude kofan yayi dakinta kamshin turarukanta yakai hannu ta kunna wutan dakin, dakin yayi haske yakalleta tarufe har kanta, dan sassauta muryansa yace “kinyi dinner?” Shiru tayi kaman tana bacci, folding hannunsa yayi akirji strictly yace “stand up” kaman marainiya ahankali tasa hannu ta yaye bargon ba dan kwali kanta ta yunkuro spaghetti hand na rigan bacci yagani red ajikinta kawai yajuya yace “come down and eat” yawuce bai rufo kofan ba, ahankali Ahlan ta tashi tana tsoron karya kara mata fada, tadauki hijabi tasaka tazura slippers saita fito tana tafiya ahankali yana zaune a falo tv a kunne laptop dinsa nakan cinyansa yana aiki tawuce dinning tabude abincin, plate tadauka tadebi pepper soup kadan tafaraci tadan saci kallonsa hankalinsa nakan laptop din. Cinyewa

tayi tamike tsaye tawuce kitchen ta wanke bowl din tana ganin plates da cup da aka wanke amma suna gefen sink ba amaidasu rak ba hanu tasa tadauka tamaidasu rak saita fito tawuce sama tabude dakinta ta shiga tamaida kofan tarufe wayanta ne yahau kara sai yanzu ta tuna dashi ta kalla wannan number ne kawai saita bude wayan tacire SIM card ta karya sim din ta ijiye akan side drawer da sauri, tazauna tai shiruuu sai kawai ta tashi tawuce bayi ta dauro alwala tazo tafara shafa'i da wuturi duk addua tayi ciki, for Ummy ta saikuma ita tama kanta addua Allah ya daidaita rayuwanta she really miss being happy Allah yazaba mata abu mafi alkhairi, wajajen 11 saita tashi ta core hijab da dadduma ta links ta ijiye saitahau gadon ta kwanta tana hamma ko 5minutes bata karaba baccin yadauketa bata kashe wutan dakin ba.

Wuraren 12:30 Habeeb yagama aikin dayake yatashi yakashe kowani wuta yarufe kofa yataho sama zai shiga dakinsa ganin dakinta akwai haske saiya tsaya knocking kadan yai amman shiru hakan yasa yabude kofan ahankali batare dayabar kofan yayi karaba ya ganta kan gado this time around she's really asleep ta rufe da bargo sosai AC ta na 17, kaman zai fita saiya shigo remote yadauka yarage AC yamaida shi 25 zai juya saiyaga SIM card nata ta karya da wayanta asaman drawer tsare abin yayi da idanu saiya taka zuwa wajen, hannu yasa yadauki wayan saiya danna screen din wayan a kunne dudda ba sim but yaga about 57 miss call ga messeges ga WhatsApp message swiping yayi yaga ba password, yabude kiran yaga is same number saiya shiga messeges din yana karanta message din daga farko wanda gabaki daya threat ne. "Kika auri Habeeb saina kasheki koda kina cikin mahaifiyarki ne kin sanni sarai" sender baiyi revealing identity dinsa ba but from the text messages he understood ita Ahlan tasan waye ke mata sakon, watsapp nata ya shiga same number same threat, sai another different number yatura message bata duba ba, Habeeb ya danna yabude. "I feel kaman rayuwana tazo karshe, Ahlan ina sonki sama da komi na duniya, why why why did you get married to someone that doesn't love you or know your worth? I love you and I know you love me, I'm the right man for you, I will never stop loving you" Dr Ashraf yagani akan sunan number wanda WhatsApp ke nunawa dan ita batai saving number ba, zafi kirjinsa yashigayi kaman an zuba barkono saiya fita yawanci yan scrolling, daga Husna sai Ummy sune kadai a chat box nata, dan juyowa Habeeb yayi ya kalleta shi kansa baisan meyakeji ba, saiya dauki wayan da SIM card din yakashe wutan dakin yawuce yafita.
EPISODE 41

Around 5 na asuba Habeeb yatashi, wanka yayi as usual yafito agurguje ya shirya yafito haryakai bene yadawo yayi knocking kofarta sau biyu saiya juya yafita, bude idanu Ahlan tayi tana addua, tasauka daga gadon tashiga bayi tadauro alwala tafito tai salla, tai azkar, tunawa da yau Monday dasauri tadauko jakan school nata da case files dake hannunta da har yau batai assignment dinba da labcoat nata ahankali tafito tasauka kasa ta ijiye afalo kan table cus tanaso yasan tanaso taje assibiti, daki takoma danta fara shiryawa.

Wajajen 7 na safe Habeeb yashigo yamaida kofan yarufe yana kallon school bag, hospital case files da labcoat nata dake wajen kawai yawuce abinsa sama yashiga dakinsa, Ahlan dataji shigansa daki kirjinta yadinga bugawa batasan taya zata gayamai zata school ba, wani milk silk material gown tasaka tai rolling gyale milk color ba kwalliya fuskanta tai kyau lips nata kaman tashafa pink lipstick kuma ko Vaseline bata sakaba, gajiya tayi da zama, wajajen 7:45 tafito ahankali tamaida kofan tarufe tasauko kasa ta zauna tana kallon sama har 8, mikewa tayi ahankali tashiga

hawa staircase zuwa sama agaban dakinsa ta tsaya takasa knocking, da kyar takai hannunta tai knocking ahankali, shiru, bayan kusan 1monute takarayi daga ciki akace “come in” bude kofan tayi kadan wani sanyi kaman kankara da kamshi yadaki hancinta dakin duhu, ahankali tace “good morning” bai amsaba kai tsaye yace “why are you knocking”? Tarasa mezatace tai shiru, strictly yace “if you don’t have anything to say shut d door”muryanta na rawa sosai cikeda tsoronsa da shakkan sa tace “can…..can….i go to the clinic Yaya….”? Yanda tai maganan was so heartfelt saida yaji har azuciyansa especially yanda tace Yaya, dan jim yayi chan yace “wani clinic?” Ahankali tace “I…..I’m doing practical a general hospital” shiru yayi chan yace “how will you get there”? Asanyaye tace “zanyi bolt” kaman bazaiyi magana yace “wait for me” ahankali ta gyadamai kai ko kadan bataso ya kaita tace “uhn” tajawo kofan ahankali tajuya takoma falo, labcoat nata tadauka ta warware tasaka ajikin ta maida boturan tarufe, tadauki jakanta ta rayata a shoulder tadauki, hospital case files din a hannu taga crocks black da aka ijiye mata a gaban flat dinnan shi zata saka tana tsaye taji yabude kofa batai gigin dago kanta ba, yana sanye da 3quater black sai black shirt yayi kyau jikinsa a mummurde, black dinsa na kyalli, kallo daya yamata yadauke kai yataho yadauki car key kan table yai kofa yafita batare daya mata magana ba dasauri tabude kofan tafito harya wuce, takalmi tasaka yawuce wajen parking motoci yana bude motan yadan kallonta tana tahowa bugawa kirjinsa yayi tamai kyau dasauri yadauke kai yashiga motan zuwa tayi wajen motan ahankali tabude asanyaye batare data kallesa ba dayar karaman baby voice tace “naje na gaida Ammi”? Dan kallonta yayi kanta akasa tana wasa da fingers nata yadauke kai, kaman bazaiyi magana ba yace “you have 1minutes”dasauri ta ijiye jakanta da case files din tajuya tai flat na Ammi dasauri harda dan gudu, Ya Sadiya dake window tareda Ammi suka koma dasauri suka zauna suna hiran karya, ahankali tabude kofan tashigo da sallama ahakali tadan duka tace “ina kwana Ammi zan tafi school, ina kwana Ya Sadiya” atare suka amsa Ammi tace “Masha Allah adawo lafiya karfe nawa kuke tashi”?ahankali tace “5 ko 6 depending idan munada surgery” Ammi tace “tom maza sha wannan ki tafi” karba tayi tsumi tasha dawani magani da aka dama da yoghurt tana gane baki tawuce tafita ta tafi wajen mota tashiga ahankali yarufo kofan Habeeb yaja motan sukabar gidan, Excellency dake sama yayi wani murmushi, ahankali yace “Alhamdulillah”.

Hanya take kallo gabaki daya she’s not comfortable in the car ahaka sukakai hospital din yashiga yayi parking tadauki bag din da case files zata saita tsaya murya chan kasa tace “thank you” takai hannunta zata bude kofan kaman daga sama yace “when is closing time? And where is ur station?” Yayi magana authoritatively, kanta na kasa tace “4,5,6 shine closing time depend on idan muna operation” tadanyi shiru lips nata na motsi yace “uhn” asanyaye tace “ina trauma surgery but maybe na chanza yau” baice komiba hannunsa yasa a Aljihu yazaro wata iphone 17 plus ya mika mata yace “here” dago kanta tayi ta kalli wayan saitasa hannu ahankali takarba tace “nagode” tabude kofa tafita tamaida kofan tarufe tashiga tafiya hakanan samin kansa yayi da binta da idanu zuciyansa na tafarfasa, harta shige building din yakasa kunna motan yatafi, kawai his head keeps bringing hoton mutumin nan daya bangajesa awajen daurin aure, wanda yaga Dr Ashraf jikin rigansa, he saw text from him jiya on her phone, dukan sterin mota yayi yace “what is wrong with you Habeeb?” Babu anything like love tattare dakai, but then mesa yakejin zafi yana tunanin she is with that man working with him? And so? Sonta kake, deep down kawai shi mutum ne mai balain kishi it doesn’t matter ko yanason abu ko bayaso kawai abunsa abunsa ne forever, as a man duk wani abu da akace nasane shi kadai yakeso yaga yanada iko da abunnan, baison Ahlan baison auren but still as long as akwai this auren he wants to be the only man in her life, kawai bai yarda kowani namiji na kula abunsa ba ko yana kallon abunsa ba, da gaske kawai yakasa tada mota yabar wajen.

Building na CMD Ahlan tawuce cus tasan ana ake zuwa idan kanada any complain kowani abu, office din tashiga secretarytace “are you here to see CMD Dr?” Gyadamata kai Ahlan tayi, Secretary tace “I’m afraid you have to come later she’s not here yet” gyadamata kai Ahlan tayi tajuya tafita, tafito tawuce wajensu ba lallai Husna ta iso yanzu ba sabida da school bus suke zuwa agaban office dinsu ta tsaya hakanan gabanta yafadi tunawa datayi da Dr Ashraf bude kofan tayi ahankali Dr Ashraf na zaune kan table dinsa shi kadai sauran basu iso ba yana rikeda file ga bandage a goshinsa, yarame sosai, yayi wani iri, looking very rough, idanunsa sun fada ciki sunyi zuru zuru, dago kansa yayi hakan yasa dasauri tasauke kanta kasa sai kawai tajuya zata fita strictly yace “you can’t avoid me forever, atleast i deserve some sympathy from you Dr Ahlan, i deserve an explanation with a sorry, I’m human remember” yakarasa maganan muryansa na breaking kaman zaiyi kuka, chak Ahlan ta tsaya kawai zuciyanta ya katse taji yabata tausayi zuciyanta yayi wani rauni kawai saita daura hannuwanta akan bakinta tana taushewa tana hana kanta kuka ahankali tace “I’m sorry I’m so so sorrryyyy” hannunsa tagani akan kofan yamaida yarufe dasauri tadago jajayen idanunta ta kallesa idanunsa sunyi ja tana komawa baya ganinsa kusa da ita, ahankali yace “don’t cry Ahlan, are you happy?” Ya tambayeta cikin wata kalan murya dayasa tasake fashewa da kuka, dan lumshe idanu Dr Ashraf yayi yace “Ahlan you are an adult kinada right ki zabi abinda kikeso, your father can not just wake up ya aura miki wani wanda baki sani ba, I know you love me, I love you too, it’s not too late break this marriage let’s leave go somewhere else and get married”
Lumshe idanu Ahlan ta fuzar da iska saitakai hannu ta goge fuskanta tass ta kallesa ahankali tace “yes I don’t know anything about auran nan, bazan taba iyama Abbana abinda kake cewa ba, I can’t leave this marriage kona gudu dakai naje wani waje, kayakuri Dr Ashraf Allah yabaka mata tagari” files din hannunta tamika masa tace “this are your files zan sami CMD I’m changing department I can’t work with you when I know you have feelings for me ina matar aure, ba kyau”tunda take maganan Dr Ashraf yake kallonta harta gama kaman zai mutu yakeji saiya juya kaman mahaukaci yaje table nasa yadauki wani small surgical scalpel yakalli Ahlan da kanta ke kasa yace “dani zaki rabu Ahlan? well look this is the easiest way, I’m making it easy for you ki rabu dani ki daina ganina forever basai kin chanza department sabida ni ba” Ahlan ta kallesa kawai yasa wukan a gefen wuyansa ya danna saiga jini, zaro idanu Ahlan tayi tace “Dr, Dr, Dr wat are you doing?” Murmushi yamata yace “helping you to get red of myself for your sanity and peace” kawai yasa wukan wuyansa yafara yankawa ga jini tsirrrrr, wani ihu Ahlan tayi. “Dr Ashraf” aguje taje wajen takai hannunta duka biyun tadaura saman wuyansa tana hana jinin fesowa jikinta gabaki daya na shafan nasa……
EPISODE 42

Ko 1minute Ahlan batayi da fitowa daga building na CMD ta shiga dayan building dinba motar school bus nasu ta shigo asibitin, motan Abbanta biye da school bus din dan tun jiya yakasa bacci, yakasa runtsawa, yasaka sukuni, idan yatuna yau Ahlan zataje hospital kawai saiyaji hankalinsa natashi, bawai baiyi trusting Ahlan bane but baiyi trusting doctor nan ba yariga yagane baida hakuri kuma irin mutanen nan ne da basu iya soyayya ba, basu da control a zuciyansu.

Har lokacin Habeeb na zaune cikin mota shi bai fito ba, shibai tafi ba, yaga motan Abba tayi parking, yagane motan sabida plate number motan abin yabasa mamaki what is Abba doing here? A chan gaban entrace kusada school bus din motan Abba yayi parking, da kansa yasauko baijira bodyguard dinsa yabude masa kofa ba yatafi wajen school but din ya tsaya gefe yana kallon masu saukowa yana jiran Ahlan ta

sauko saiga Husna dasauri tace “Abba ina kwana” Abba yawashe baki yace “daughter na ya gajiya, ina kawarki Ahlan?” Husna tace “bata zo ta bus ba, I tried her line bai shiga ba maybe ta iso tana departm…” katseta Abba yayi dasauri yace “kaini department din datake i need to see her” gyadamasa kai Husna tayi tai gaba Abba yabita abaya dasauri yana gyara babban rigansa, Habeeb na zaune yana kallonsu bai fitoba cus baimaso Abba yagansa, yarasa what exactly is keeping him there, what exactly ke hanasa tafiya, jikinsa wani iri yake masa, suna shiga building din kuma sai kawai yaji yataba kofan motan yabude yafito yamaida yarufe, saiya shiga tafiya.

Daidai Ahlan tadaura hannunta a wuyan Dr Ashraf dake fito da jini jikinta na shiga nasa aka bude kofan office din Husna ce tashigo Abba biye da ita! Yanda Ahlan ke cikin tashin hankali kanta baimaji karan bude kofa ba, bakinta motsi kawai yake tana kallon Ashraf da idanunsa sukai ja yana kallonta hawaye nabin gefen idanunsa tana girgiza masa kai tana cewa. “I will not leave y……” “Ahlan!” Taji muryan Husna na kiranta dasauri tajuyo, kasa karasa maganan Ahlan tayi ganin fuskan Abba, Husna tazo wajen da gudu daidai Abdulrazak da Monica na shigowa office din Habeeb tsaye bayansu idanunsa akan Ahlan da Dr Ashraf, cikeda jarumta Husna tai kan table na Ashraf tadauki bandage tazo wajen da sauri takalli Ahlan data kankare wajen, wani tsawa ta dakama Ahlan. “Cire hannunki daga wuyansa!” Afirgice Ahlan tai yunkurin zare hannun, Ashraf yakai hannunsa yarike hannun Ahlan dake wuyansa yana kallon Abba yace “this will keep happening harsai kun cire Ahlan daga auren politics dinnan dakuka mata bataso Sir……” Dr Ashraf yayi maganan yana kallon fuskan Abba, cikin murya mai rauni yace “I….ina son Ahlan da inhar bazan sameta ba gwara na mutu na huta…….” What are you waiting for?” Sukaji muryan Habeeb wanda da sauri Monica da Abdulrazak dake gaban kofan suka matsa fuskansa ya bayyana ya tsaya chak hannunsa zube cikin aljihu yana tsaye cikeda kwarjini da izza dawani irin cika idanu ga tsantsan kyau da aji ba, idanunsa kadai Ahlan ta gani ita kanta batasan sanda ta fizge hannunta daga rikon da Dr Ashraf yamata ba, saiga jini dasauri Husna ta daura bandage din a wuyansa, Habeeb yashiga takowa yana shigowa office din Ahlan najin takunsa har cikin zuciyanta, Dr Ashraf dake tsaye nawani irin kallon Habeeb, dasauri Ahlan tawuce tai bayan Abba ta tsaya jikinta na bari takasa kara kallon Habeeb, Ashraf ya kalleta yanda taboye bayan Abba saiya kalli Habeeb, Habeeb na tsayawa wajen, cikin wani irin banzan hali na usulin I don’t care yace “leave him alone let him bleed out for all I care, I hope carotid artery ka yanka, so you don’t survive” kowa na dakin saida ya kalli Habeeb hatta Husna jin abinda yafadi, dasauri Husna tasakesa saita matsa baya, Dr Ashraf yayi wani murmushi saiya kalli Abba yace “can you see the monster daka aurama Ahlan wanda baida imani for mankind and humanity”? Strictly Habeeb yace “mind the way you talk to my father! Watch lafazin ka or you loose your tongue!”wani dukan uku uku zuciyan Dr Ashraf yake, yace “yes but ai baka da imani, tayaya mutum mara imani da tausayi zai rike Ahlan? I have to put it out to Abba”cikin wani banzan murya Habeeb yace “don’t brother sunfi kowa sanin waye ni, yet I got the girl not you pinky hear!” Bura’uba maganan tama Dr Ashraf ciwo shi Habeeb ke kira da mai zuciyan mace, pinky heart na nufin girly heart, azuciye Dr Ashraf yaduka yadauki scalpel dagudu Abdulrazak yazo zai shiga tsakaninsu da hannu daya Habeeb yasa ya fizgo Abdulrazak kaman fly strictly yace “stay where you are!”Abdulrazak baitaba jin ya tsorata dawani kaman Habeeb ba arayuwansa yanda yakamasa yacire daga gabansa kaman yacire tsuntsu, Monica tajuya dasauri tafita ganin ayanda taga Habeeb zaima Dr Ashraf shegen duka ne cus that man looks like soldier, Abba ganin abin zai escalating ga Habeeb da bakin zuciya jibi yanda yadauke student yaron chan Abdulrazak yasa yace “Habeeb, Alameen, kaga let’s go” ko kallon Abba Habeeb baiyiba yakalli Dr Ashraf da wukan yace “I’m waiting, come” Dr Ashraf baiyi motsi ba yana kallon yanda Habeeb ke kallonsa yana jiransa, cikin muryan wanda yasan he stand no chance da Habeeb yace “you know what no nafasa Ahlan is here I don’t want to traumatize wacce nakeso, I am not you, but tsaya kaji” daidai ana bude kofan MD da zuwanta kenan Monica takirata harda

dan gudunta ta shigo idanunta kan Dr Ashraf da jini kebin wuyansa ga scalpel a hannunsa ta taho da gudu tace “Ashraf, Ashraf son me kake haka what is happening? Innalillahi, kwana nawa ina nemanka? Rabonka da gida tun Friday? Saisa I was late to work today I had to report you missing a police station, wat did you do to yourself eh Ashraf, Ashraf look at me Mom is here, Ashraf” MD tai maganan tanakai bakin gyalenta tana daurawa wuyan Ashraf idanunta sun cicciko da hawaye tama rude gabaki daya, Habeeb ya kalli matan kawai he felt wani iri cus he could see pain nata, saiya juya yashiga tafiya, cikeda zuciya da daga murya Ashraf dako kallon mom dinsa baiyiba yace “where are you going? Are you scared? Why are you going? Toh bari kaji, zuciyan Ahlan will always belongs to me!” Chak Habeeb ya tsaya, MD ta kalli Habeeb saita shiga kallon mutanen office din ga Ahlan bayan babbanta, dasauri Mom tace “Ashraf wat are you doing are you mad? Innalillahi Ashraf hauka zakayi ne eh, stop talking, stop being disrespectful, stop looking for trouble” kaman badashi Mom ke magana ba yace “she will always love me, you might be her husband but you are nothing but the name, Husband, Ahlan ni kadai takeso, we have a connection, you need to see how scared she was dataganni bleeding she thought she was going to loose me, zaka gani I will make her get out of this political marriage, Ahlan is not a toy dazakuyi amfani da ita for personal purpose naku, she’s a woman that deserves to be respected, she deserves to be heard, her opinion and choice matters!” Dr Ashraf yayi maganan yana kallon Abba da Habeeb din daya tsaya, CMD da hankalinta ya tsananin tashi ganin Ashraf lost it completely tace “Innalillahi dan Allah kuyakuri, dan girman Allah, I’m sorry on behalf of my Son, Alhaji rabona dashi tun Juma’a, nemansa muke badare ba rana, I’m not sure if he has eaten, he’s not okay, this is not how Ashraf dina yake, he’s not okay” ihu Dr Ashraf yayi yace “I’m okay my heart is not okay sun cuceni, Mom kice ya saketa ba sonta yake bafa, mugunta aka mini, baya sonta why is he staying with her, yasaketa nidanake sonta na aura Mom, inason Ahlan, everyone I love Ahlan, hospital, patient, people, student I love Ahlan, kuraba AUREN HADIN nan na aureta, I love Ahlan I love love love Ahlan!” Yarabi Dr Ashraf ya haukace kawai jikin Ahlan har tsuma yake sabida kuka, CMD tafashe da kuka tana kai hannunta bakinsa tace “Ashraf, Ashraf, Innalillahi, Ya Allah I’m alone babansu jarasu karka jarabce ni da new jarabawa, Ashraf”.

ALLAHU AKBAR DR ASHRAF😭
EPISODE 43

Kowa na dakin jikinsa yayi sanyi, Ashraf is still talking kawai CMD tasa hannu ta danne bakinsa ne yasa ba’aji, Ahlan was crying, bata tabajin taji tausayin Ashraf kaman yauba, Habeeb jikinsa yayi sanyi, kawai Maman Ashraf tabasa tausayi not even the Ashraf, baiso yaga iyaye na cikin damuwa ko suna wahala it affect him so much, kawai yawuce yafita, idanun Husna sunyi ja Dr Ashraf ya haukace wlh.

Juyowa Abba yayi yakalli Ahlan dake kuka abayansa yasa hannunsa yakama hannunta kawai yashiga tafiya da ita Ahlan na binsa tana kuka tana kallon Dr Ashraf da Mamansa sun balain bata tausayi zuciyanta ya sosu sosai suka fita.

Mom takalli su Monica tana goge fuskanta tace “the rest of you go back to A&E” suka wuce suka fita saita kalli Husna dake tsaye idanunta sun ciko da hawaye tana kallon Dr Ashraf dake huci yana kallon kofa idanunsa sun chanza launi like he’s not himself, Mom tace “go back to your unit” gyadamata kai Husna tayi tashiga tafiya hartakai

kofa, asanyaye Ashraf yace “Husnaaaah!” Juyowa Husna tayi ta kallesa da sauri, dukawa Ashraf yashigayi jikinsa babu ragowan karfi, ahankali yace “I….I love Ahlan Husna, bansan menake ba, i don’t know what I’m doing, inason kawarki sama da rayuwana, help me Husna, can you help me please Husnaaaaah”wani nauyi Husna keji azuciyanta na tausayin Ashraf, zuciyanta ya tsinke gabaki daya, MD ta kankamesa. Kirjinta tace “Ashraf what are you doing to yourself? In all this things kana tunani na? Kaida Sister ka are all I got, mahaifinku yarasu, ina zansa kaina wani abu yasameka eh? Look at you? 3days bakazo aiki ba, are you trying to loose your job? Komi kaddara ne, kayi tawakkali kayi hakuri sai Allah yasaka maka da abu mafi kyawu da albarka, baka auri Ahlan ba sabida haka Allah yaso haka Allah ya kaddara, you wife is somewhere out there, trust in Allah bazaka tabajin kunya ba Uhn Ashraf” juyawa Husna tayi dasauri kawai tafita daga office din da gudu, wani bayi tashiga kawai taduka tadinga kuka, jikinta ko’ina rawa yake karkarkar tana kuka, kawai she likes Dr Ashraf, Allah ya dauramata sonta daga rannan daya fara tsareta ya tambayeta meya sami Ahlan bata concentrating, da rannan dayasa tabasa number Ummy, da rannan daya biyota masallaci, kan tabasa number Ahlan shine rannan data fara sonsa wani kalan love triangle ne wannan? Tayaya zuciyanta zaiso wanda keson kawarta? Tanason wanda ke son kawarta datai aure? she’s not sure idan Ahlan na sonsa Ahlan is more like tausayinsa takeji da sauransu but ita she seriously love him, she’s in love with Dr Ashraf, wannan wani irin love triangle ne, he’s hurting she’s hurting even more, what can she do to help him? Tayaya zata zama mafita arayuwansa? Tayaya zata maye gurbin Ahlan a zuciyansa? Tayaya zata cike ta void? How can she make him look at her for once da idanun soyayya? Dr Ashraf is a good person, he’s not evil, she loves him and she promise she will help him.

Psychiatrist MD takira cus her son really needs counseling yafara attempting self harm, allura akamai sai aka sashi agado aka fita dashi daga office din, Husna tafito daga bayi tabisu Mom takalli Husna, ganin idanun Husna harsun kumbura sabida kuka wnada she’s sure abinda tafita taje tayi sai kawai ta barta, suka tafi dashi ward din.

Tunda suka fito waje motarsa Habeeb yawuce wlh ko waigowa baiyiba kawai ya kunna motan yafita dawani shegen gudu Abba yawuce motansa da Ahlan ganin Habeeb yawuce yabude motan yadaka mata tsawa yace “shiga” shiga ciki tayi Abbayashiga motan security dinsa yarufe driver yaja motan Abba yace “all I think I though bama kisan mutumin nan ba but ashe kinsansa da aurenki, daga zuwanki hospital din kikaje kina magana dashi, to bari kiji dagayau na yanke zancen school din, kin gama makaranta” hannu Ahlan tadaura akan fuskanta tana kuka tama kasa magana ahaka sukakai gidan har compound din, direct riketa yayi zuwa flat din Excellencu Abba yabude kofa, Excellencu yamike yace “Subhanallahi wat happened? Ahlan why are you crying”? Abba zaiyi magana Excellency yace “wait wait calm down” yakalli Ahlan dayaga blood all over her hand yace “wuce tafi flat dinki i will come and see you later” juyawa tayi tawuce tafita.

Excellency ya kalli Abba yace “what is happening?” Abba yace “I told you Excellency ni zuciyata bai natsu da wanna likitan ba, yazo wajena, yazo wajen daurin aure, zuciyata keeps telling me someone like him bazai kyale maganan ba, kawai i decided naje asibiti nabi bus nasu suna saukowa naga Husna nace takaini wajen aikin Ahlan naje muka shiga kasan I met yarnan da hannayenta biyu a wuyansa ya yanke kansa wai zai kashe kansa idan bata dawomai ba”Excellency yace “Subhanallahi!” Abba

